atake gidan sankiran yarikice baye inna HADIZA mahaifiyar Nura tafi Nura shiga damuwa sai tsinewa Hamrah suke atake suka had'a baki suka ciwa kabiru kurma mutumci Yau kam har Baba Haruna me bin bayan su bai yi magana ba

Koran Kare sukayiwa Kabiru da iyalin sa wai suji yanda Nura yaji kafin su maka Hamrah a kotu

Juwairiya ta kira Wassileem ta ke gaya masa dariya Wassileem yayi yace "ai Juwa haka nake so su koremun ni dama ina tunanin yanda zan zo na sauka a wannan k'azamin Gidan

Bari na kira Mujashid yanzu zai zo ya kai ku gidan da YA Sahal ya gina mana

GIda ne na garari a cikin shagari Sahal ya ginawa iyayen Hamrah inna Dumba da Kabiru basu ta ba shiga irin wannan GIdan ba fur suka dage bazasu shiga ba saida Juwa tayi ta rokon su

Ansa ranan auren Juwa da Akkram Wassileem da
Ammatee Allah Ya d'au kaki family Kabir Sanki

Agidan yan ukku
 Hamrah Sahal
"my Sahal yanzu tafiya zakayi".

"haba my baby kema kinsan ba dan da Mal zamuyi tafiya ba da dake zan tafi to nasan halin sa Wllh zai iya wulakanta min ke."

Nunfasawa Hamrah tayi tace "narasa meyasa danginka suka kini Wllh idan suka yarda na aure ka zan musu biyayya musamman umma da Mal nasan sune matsala na."

"Hamrah lefin ki me girmane wanda ban ga lefin Umma ba dan ta hanani auran ki ba uwar da zata so d'an ta ya auri irin ki amma mu barwa Allah ikon sa
Dan ni nakafe Sai ke

Shima Mal bashi da budurwa wai wata yagani sama da shikara 6 wai ita yake nema shine basu matsa nin ba amma da Mal yayi aure nasan ba zasu barni ba."

Hamrah kwance tana chatting da wani saurayi da Ya nace shi sai ya aurare ta

Ruwaida tafito cikin wani arnen shigan ta wanda ba za ka taba cewa tasan muslumci ba

tazo dai dai kan Hamrah tace "wai ke ba zaki fita bane?.

" kai bana jin fitan nan amma ga check ku biya bank saboda da safe muna da zuwa Gidan marayu."

Hamrah tayi maganan tana mekawa Ayya check
din

Abdullah da Barrat ne suka ce Momi zamu."

Ruwa tace "ah ah kuje Cabaliya ta muku wanka Sani ya kai ku kusha ace cream ."

Barrat ta turo baki dan tana son fita dasu Abdallah kuwa murna yayi sosai

A bank jama a sunyi yawa kasan cewar karshe wata ne amma da yake su Ruwaida idon duniya ne atake a ka karbi check din su ajiye cek din yayi akan teble sai de dawani cek din awaje bayan yasa hannu a wandan yake hannun sa ya dauko na wasu Hajiyoyi da suka fara meka masa
amma Sai yaga check din iri daya ne da nasu Ruwaida hakan yasa ya kasa tan tacewa dan duk signed din SA IDU M WALWALA ne

Ya dago

ya "Kalli matar yace HAJIYA ai check din naku yazo daya da wannan kode tafiyan ku daya ne na kasa gane wanda ki ka ban."

da sauri matar tace "manager ban gane ba muga.
 tana garba taga check din Sahal ne tare da signed din sa

"waya baka wannan din." yace gasu."
 yanuna Ruwaida da Ayya

"ke ina kika samu wannan cheick din?

Ruwaida wani kallo tayiwa matar wanda kana gani kasan uwar Sahal ce
tace mata "dan me zaki min wannan tambayar."

Matar tace "saboda d'ana ne."
"ok na kane Hajiya Turai ce."

"to ni kuma budurwar sace me jirar sa dadi ."

Hjy Turai tace "Budurwa ya d'auki wannan magudan kudin ya baki Wanda ya linka nawa."

Ruwaida dariya tayi tace "to banda ke da abinki Hjy saurayi na nefa dan yabani fin haka ma ai ba a bin mamaki bane Yana bani fin haka ma ya zaiyi ya baki abinda yake bani kina masa abinda nake masa ne."

Hjy Turai ido ta zare ta kasa magana

sai matar da suke tare ce tayi magana dayake su ukku ne suma amma dayan

da nikaf
a fuskanta
Matar tace "ke wacce iriyar suruka ce har zaki dubi sabar idon uwar sa ki fadi haka ."

Ruwaida ta juyo ta kalle ta tace
"dena cewa surukata uwar saurayi nade wanda ta hana hallal bata hana Haram ba ta hana muyi aure amma bata hana ya rage zafi dani ba
ki gaya bata tayi kuskure dan ni da natashi har da iyayen sa maza na hada nake harka ".

Matan duka ukku suka hada bakin cewa "kece Hamrah."!!!!!!!

"ummm.
tace

me nikaf din tace "lalle baki da kunya ahakan kike son d'an namu ya Aurer ki ai ko mata sun Kare ba yanda za ayi Sahal ya auri karuwa irinki."

Dariya Ruwaida tayi tace "me ya rage ai ina samun yanda nake so awajen d'an da uban dan ba da Sahal kadai nake har kar ba hadda k'anin baban sa Wakili walwala
kai har Iddeeri da Hakuna zan hada dan yanzu haka cikin su ne dani idan na haifu nakai muku Sai kutan tance na Sahal ne ko na iyayen sane....

Wani mari me nikaf din ta zuba mata
aiko ita ma ta d'aga hannu zata rama
Ayya ta tare hannun

Ai take hankalin mutane yazo kan su

Kuka uwar Sahal take matan 2 suka jata suka fita ko check din basu tsaya sun karba ba

a mota sai fad'a Ayya take mata har suka k'a raso gida

Ruwaida Sai kace da tayi abin arziki da gudu ta karaso ta rungume Hamrah

tace sister Albishirin ki."

"goro."

ai Yau na miki maganin wannan muna fukan matan."

"suwa?

Uwar Sahal mana da matan k'annen baban sa duk naci mutum cinsu."

daga nan ta kwashe yanda akayi ta gaya wa Hamrah

Hamrah mekewa tayi
Cikin hawaye
tace "amma Ruwaida ban taba sanin ke yar iska bace sai yau ko ma meye baza suci darajan Sahal ba kiduba yanda shi yake mutunta nawa iyayen zaki yiwa nasa haka Wllh Allah ya isa tsakani na dake."

Ruwaida cikin mamaki take kallon Hamrah ita a ganinta kwaninta tayi

"yanzu Hamrah dan na rama abinda suka miki shine zaki jamin Allah ya Isa ba nan suka kiraki a waya daya bayan daya suka ci miki mutumci ba har kina cewa muje gidan nace kibari wata rana dalili zai hadamu murama Sai da dama ta samu yanzu zaki ce haha. "

Hamrah tace "amma ai ba wannan akuyancin naki nace zanyi ba baki tsaya akan dan su ba har Mijin su."

Daga nan de suka fara fada wanda tunda suke basuyi irin saba Ayya tana kallon ba tayi magana ba balle wata tace ta goyi bayan wata

Sai Cabaliya ce tazo ta raba

"Subbahanallashi Sankira yau kune da fad'a haka."

Hamrah da kuka ta haye sama dan tasan Sahal yanda yake ji da yan gidan su zai iya b'ata musu rai ko ma yarabu da ita

Ruwaida ko ko ajikin ta wani irin tsawa ta dakawa Caballiya wanda ta kusa jika da ita tsim tsim Cabal ta fita

tunda abin ya faru Ruwaida ta rasa me yake mata dadi dan dama da Hamrah suke kulle kullen su na daukan fansan dan Ayya ba abakin komai take ba gashi yanzu Hamrah tana fushi da ita

yau ta kudurta ko bata so sai sun shirya

Hamarah tana zaune tsakiyan gado ta buga uban tagumi dan ta rasa yan da zata shawo kan Sahal yaki sauraronta ya kirata ya gaya mata maganganu son

ransa

ita ma ayu ta kudurta dole ta sashi a idon ta
Hakan yasa takira s s din sa Jaafar
Tace dan Allah ina Sahal"?.

yace muna A W I hotel oga bashi da lafiya fa kizo nasan ke yake bukata."

"ok gani nan zuwa."

agaban Ruwaida sukayi wayan taji komai dan haka tana ganin Hamrah tafita ita ma ta shirya ta bita

"Wllh Hamrah abin ya bani mamaki yanzu a gida komai ya rushe na shirin auren mu da nake sa ran zan shawo kansu amma yanzu faruwan wannan abin yasa An samin rana da Khadija kanwata yar gidan Baba Wakili wanda na ke cemiki suna kama da Ruwaida sosai."

Hamrah rumgume shi tayi ta saki kuka

tana cewa "Wllh bazan ta ba yafewa Ruwaida ba."

bude kofan akayi Ruwaida ce ta shigo jiki a sanyaye ta zube a gaban Sahal ta shiga jera masa hakuri da kyar ya hakura

a parlour suka barta suka shige cikin bedroom
Ita kuma ta zauna dashir tana chatting da Kamal dan sun kusa d'ana masa tarko

akayi knocking tashi tayi shigan na yau yafi na kullum k'azan ta dan wando tasa da rabin cinyan tane Sai wani riga Wanda da shida babu kusan daya ne gashi da ma ita ba bra take sawa ba Shara Shara ce rigan iya cibiyar ta cibiyar ta harda sarkan cibiya das ya manne ciki gefin cikin ta an yi mata zane mekyu tare da sunanta *Ruwa Ruwa*
gashin kanta ya baje a bayanta shigan Ruwaida ko a turawa fusararun sune masu yin sa

Tana karai rayar da tasaba yanda take juya mazaunai sai kace roba ta tafi bude kofan

Nunfashin tane ya kusan daukewa a sanda taga wanda ba ta taba tsammanin gani ba kode idon tane yake mata gizo bata San santa bakinta ya furta " *SOJANA* !!!!

shima halin da yashiga har yafi na Ruwaida bude baki yake da niyar zayi magana amma sai ya gagare shi dan rawan da bakin yakeyi

Sai Ruwaida ce take Furta "wlllh shine Wllh shine !!."

ihun da take ne yafito da su Hamrah

"Hamrah zaki kansa Wllh soja nane shine."

Mal shigowa yayi
yakama hannun Sahal
Cikin in ina da rikicewa ya furta
"Sal dama Ruwaida itace k'awar karuwan ka da kake cewa suna kama da *KHARAJINA* ."?

ya juyo kan Ruwaida yace "Ruwaida ada kece farin cikina ke nake nema tsawon shekaru naje gidan me kwano ba adadi amma ake cemin ba ama san ki ba nikuma agidan na fara ganin ki cikin shiga na mutumci da ya ja ra ayina kan ki

Sai Yau da kika zo da shigan da naji duk duniya ba wanda na tsana sama dake."
yana Kai nan ya juya zai fita

Ruwaida cikin kuka tace
Yasal ka temakeni kar yatafi Wllh zan tuba yanzu na tsani karuwanci tunda shima bayansa....

Sahal kasa magana yayi

da gudu Ruwaida tabi bayan sa

"dan Allah katsaya Wllh Kai dan uwanane dan gidan Yayari ummata Ruwaidatu ni yar gidan Kharajina ce Wllh Kai dan gidan Yayar Ummata ne ita ma yar Niger ce iska ne ya hallaka danginta

Afirgice Ismail ya zuyo jikin sa yana rawa ya karaso inda take cikin in ina yace "ina UMMA KHARAJINA bata mutu ba tana ina?

"Ruwaida tace "tana nan."

Wani irin tsawa ya daka mata yace "tana ina nace."

"labarin da tsawo dan Allah ka kai ni wajen umman ka na kanta wayo ashe ita nayiwa rashin kunya na shiga ukku.... ."

Ismail ruse idon sa yayi Yana jin wani irin bakin ciki da farin cikin Ummin sa zata ga yar uwar da kullmu itace a bakinta amma bakin cikin Ruwaida ya danne farin cikin sa

Kasa magana yayi da sauri ya fara taka mata kalan benin
Ko security din shi bai jira ba ya fada mota yaja dawani wawan gudu

Haka Ruwaida ma ta taka masa baya a tare suka karasa gidan dai dai sanda su Ummi zasu fita
Kai wa umman Sahal hospital din tunda Ruwaida ta musu Rashin kunya ta ke ciwon Kai

Ismail kasa fitowa yayi a motan

Da gudu Ruwaida ta fito

Matan 3 daya da nikaf me nikaf din ce ta cire nikaf din da gani ba tambaya itace yayar Kharajina

Tace "lalle yanzu har gida kika biyo mu dan ki bi mazajen namu da yaran namu ne ko shegen kika haifa kika kawo mu tantance na waye ...

Da kuka Ruwaida ta rumgume ta fara magana "wllh Ummi ni yarki ce sunanan Ruwaida ni yar gidan Khrajina ce Wllh. "

A zafafe Ismail yafito

yace Ummi ki cire ta a jikin ki ita din k'azan tace
Kawai tayi gaggawan gaya mana inda zamu samu UMMA Kharajina ta fita mana agida."

Tofa masoya duk ina jin comment din ku Wllh *bani da network ne yasa kuka ji bana amsa* *muku Amma ni ina ganin komai posting kuma kanwata fatima jattko na turawa awayan makociyata*

YA wannan family zasu karbi Ruwaida

YA rigiman ruwaida da mommyn Affan

ya batun fansa kuwa

B JATTKO
[9/12, 10:16 AM] +234 803 970 1225: *AMFANIN SOYAYYA*
aure

NA

BATUL ADAM JATTKO
ASHBAT
JOTGAR

kainuwa asso

Inason Amfani da wannan damar wajen tunatar daku akan
Abinda yafaru da ruwaida don akwai yan mata da suke shek'e *ayarsu amma basa bari* *akarbi budurcinsu wai suna ganin budurcinsu* *shine kawai gatansu ko nace kimar su basu duba din bin zunubin da suke kwasa dan romance da suke yi shima zina ne dan awannan zamani waya kawai matasan mu na yanzu Sukeyi amma sai sunyi wanka inaga idan aka hadu gaba da gaba dan haka shima romance zina ne dan me kuke tunanin Allah bazai jarrabi Ruwaida ba*

sai batun cewa Oral sex bashida matsala dayawa mutane sun kawomin batawan cewa wai ANNABI yace matan ku gonakin ku kushiga musu ta inda kuke so to ba haka ake nufi ba

Wallashi batun gamsar da namiji ta baki ya hudanci ne abin da ake nufi da matar ku gonakin ku a na nufin kuje busu a sanda kuke so ko dare ko Rana inde ba tana cikin ibada na farillah ba ko jinin al ada ko na biki haka ake nufi

*Baki da yake da daraja zaka ambaci sunan Allah ka karanta Qur ani meyakai kazanta cikin sa al aura kazan tane dan idan kayi al wala ka tabashi

da hannu ko ba da niya ba alwala ya karyi shiko baki Kai tsaye ake budeshi a gaban Allah al aura fa rufeshi ake da yana da ts'arki ai baza ace arufe ba*

Meyasa Annabi yace idan kana cikin tsiraici kar ka bari al auran ka ya Kalli al k'iblah idan ya zama dole to ka Kare ko da tafin hannu ne sabo al aura k'azantane
Shiyasa muke gamuwa *da sababbin cutuka wanda basu bai yana a daba*

Akwai wasanni na mutsa sha awa tsakanin miji da mata ya kamata kubi ta hanyan da yadace

Ina fatan kun fashimta dan bani da network ne masu bina private shiyasa nayi wannan jawanin anan

NAGODE

16

Ummi rumguman Umma tayi ta fara kuka
da sauri Mall ya bude fridge ya dauko ruwa yana yayyafa mata taja numfashi hawaye ne yake ta fitowa amma idon arufe magana ta fara kamar haka

"ba lefin Ruwaida bane dan tayi karuwanci Wllh mune da lefi mungazawa tarbiyar tane
Muk'addam kacuce ni Ruwaida ki yafemin ba lefina bane malama da Mudda ne suka cucemu Wllh in har da gaske Ruwa ta samu wannan na kasun a dalilin zina bazan taba yafewa Malama da Mudda ba.....

Abdallah dan shekara 6 da tunda Mall yayi maganan Ruwa ba zatayi wata 2 aduniya ba yafara kuka sosai

Mall ne yajashi yace "me ya faru please mana Big Boy."

cikin kuka yace "ba kaine ba kace Auntyna zata mutu shikenan bani da kowa mom Ayya da Barrat da mom Hamrah ba sanan."

jan yaron gefe can yayi a hankali yanda su Umma baza su jiba

 yace "rabu dasu dama baka san suba barayi ne sato ka sukayi kadena son su daga yau nine Baban ka zan maka duk abinda kake so baka ga na canza maka school ba."

Haka de yayi ta yaudaran yaron har ya ware dashi

Ummi hakuri ta shiga bawa Umma
"haba Kharajina bakya ga halinda kike ciki ba ason masu Ciki suna sa irin wannan damuwan a rai
ba wani karuwanci da Ruwaida tayi sharrin doctor ne kawai
ai jinya bata inda baya shigan mutum nawane suke gamuwa da ciwon Cancer din ta hanyan abinci da abinsha musamman awannan zamanin kiyi hakuri zan bincika kinji yar uwata".

Ummi jan Mall tayi d'aki ta masa fada sosai kuma tace ban da dan uwansa Khalifa bata yarda ko Anas yaji meye dalilin ciwon Ruwa ba shima Khalifa dan Doctor ne tasan zai samo musu mafitane kawai

agidan ance de ciwon cancer ne amma ba wanda yasan dalilin ciwon

duk me imani awannan lokacin idan yaga Ruwaida sai ya zubar bata kwallah dan gaba daya kamanin tama can zawa yayi

Prof Wakili ya Kalli doc yace yanzu ka naga bawani matakin gaggawa da za a iya d'auka.?

"Sir akwai wani hospital a India sun kware wajen aikin cancer din amma fa suna rike mutum har sawon 6months

Sai sun tabbatar aikin su yayi suke bada sallama amma akwai kashe kudi."

"Alhamdulilah inde za asamu nasara ko shekara zata zauna ai kayi mana shirin tafi Ismail da Khalifa da Kharajina."

Sahal ne suna waya da Hamrah yake gaya mata Ruwaida tana asbiti
Aiko gigicewa tayi tana tambayan sa me ya same.?

"wllh dan cancer ne ya taba ta amma bai zama chronic ba ina ga zuwa jibi za afita da ita ma."

kuka Hamrah ta fara
"haba YaSall jinyar da za afita waje ne ba Chronic ba
haba nifa yawanci idan nakirata a waya bata dauka ko Kharajina ta dauka ko akashe
ashe rufata sukayi."

bata jira amsan saba ta Kashe wayan

Juwairiya ta samu tace" dan Allah sis ki gayawa Innan da Baba zamuje Kano yanzu Ruwaida ta ba lafiya."

cikin kuka Hamrah tayi maganan
Juwa tace "wai Aunty meyasa bakya son koyan kurmanci ko kinfi karfin koyane haba komai Sai kice a gaya musu mutum da iyayen sa ba zaiyi magana dasu ba."

"zan koya mana yanzu de jekiyi abinda nace."

tayi maganan tana dialling number Ayya

Ayya tana picking tafara

 cewa "mutanen nan kum fa samu lafiya tun dazu ina miki magana har kika sauka baki min Ripley ba
damma kwara ke akan shegiyar yarinyar nan Yau kwana 2 banji ta ba idan nakira ace wai tana bacci wato ta samu danginta ko idan kin sameta ki mata maganan an fitar anko amma nace Sai Kunzo kunga tunkun Abu yana karatowa fa kuyi shiru."

"Aunty Ayya Ruwaida ba lafiya yanzu YaSall yake gayamin amma ni yanzu zan fita zuwa kanon."

afirgice Ayya tace "me meya sameta."

"ban sani ba mude hadu akanon."
 ta kashe wayan
ai atake ita ma Ayya ta gayawa Mama da yake jirgi suka biyo har suka riga su Hamrah zuwa

sai dare bayan iyayen sun koma gida daga Ruwaida sa Hamrah da Ayya da Kharajina dan su Nafi ma cewa akayi su tafi sunyi yawa

har yanzu Hamrah kuka take

Ruwaida "cikin karfin hali ta fara magana

"yanzu jinyan da na kwaso na kawowa iyayena kenan da tun ina bariki ya sameni Wllh da ko gawata ba zan yarda su sani ba
Ashe Cabaliya tana da gaskiya da take rashin lafiya taki fadan inda danginta

suke."

Kharajina tace "wacece kuma Cabaliya."

Ruwaida tace "Cabaliya me aikin muce wanda ita muka barwa gidan muna hotoro munyi zaman shekara 4 amma har muka rabu bata gaya mana inda danginta suke ba

Haduwar muda
Gaballiya

wata rana munje anguwan takwayen ruwa akwai wani GIdan karuwai awajen ja ama an da muka gani ankewaye wata mata kudaje Sai binta yasuke da gani tana cikin mawuyacin hali na rashin lafiya dan gaba daya a rame take kamar skeleton matan sai masifa suke mata su sun gaji da ita tana musu wari a gida ba irin wulakancen da basu mata ba har da tona rami idan bazata fadi inda danginta suke sun Kai taba sai sun binneta amma tayi dariya

tace ita su binne ta yafi mata sauki ba zata taba komawa gida ba

Muda muke cikin mota muna ganin duk abinda sukeyi

kuka Ayya tasa tace yanzu sis wata rana muma idan maza suka dena yayinmu haka zamu koma ko na tsani bariki Allah Yana gani ba nida mafita ne da wajen zuwa."

Ruwaida tace "hakane dama ai kudin bariki ba shida albarka kuma duk karshe bariki haka ne

Ayya ceta nace sai mun temaki matar ko muma wata rana zamu samu wanda zaiji k'an mu

dakyar na yarda sabo da banason talaka a ganina macutane tunda kashi malama talakace a ka aurota taci amanan Babana haka Tabawa talakace taci amana

Amma Ayya da Hamrah suka lallasheni akan muje mu temaka mata

Muka sauka muka karasa inda suke nikam toshe hanci nayi sabida wani wari kurajen jikin matar yake

matan wajen muka tambaya Meya faru

daya daga cikin matan ne tace "wannan da kuka gani tafito cin kasuwa kuma

ta gama ci amma lokacin komawa gida yayi taki ta koma kanjamau ne da ita ta fadi garinsu mukaita taki har kudi muka ajiye Har dubu dari 500 dan kar ta tafi a tsiya amma taki ta fadi garin su mukai ta metake son mumata taci ka mana gida da wari shine zamu binneta."

amma marar lafiyar bakinta bai mutu ba sai cewa tayi
"bazan fadi ba abinda ya koroni a garinmu yafi halin da nake ciki ko gawata insha Allah dangina ba zasu gani ba."

Ayya da kuka ta cicibi matar ta sata amota

niko na dinga masifa akan me tasa mana ita a mota ko motan ban hau ba nakira Sani yakawo min mota

su kuma suka kai Cabal asbiti

Sun biya kudin komai har dana nurse din da zasu kula da ita
.haka duk bayan kwana 2 sai sunje dubota aka daurata akan magani da yake tana samun kulawa ras ta tashi har aka bata tsallama da haradin zata na karban magani idan ta kula zatayi rayuwa kamar kowa

Ba irin lallamin da basuyiwa Cabaliya ba akan ta fadi danginta mukai ta
 taki
har labarin mu suka bata amma dariya tayi tace Wllh naku me sauki ne nawa bazai fadu ba sai lashira

haka suka Hakura suka kawo mana ida gidan

da suka shigo da ita ba irin masifan da banyi ba amma basu kula ni ba

Ashe nima zan shiga irin wannan halin Wllh inda abariki nake bazan zo iyayena suga halin da nake ciki ba ahe Cabaliya tana da gaskiya."

Kuka tasa sosai

Kharajina
tace "toke sister in banda abinki kina tunanin zaki ci bulus ne ai ba ayiwa Allah dabara gashi Virginity din naki da kije tattali bai miki amfani ba wata kila ma kinyi loosing nasa tunda ance sai an miki aiki a mahaifa."

"Kharajina idan bazaki fadi abinda zai kwantar mata hankaliba ki mana shiru kawai."

Inji Hamrah da taji ciwon maganan Kharajina

Kwance yake ruf da ciki kafafuwan sa a sama sai kad'asu yake akan makeken gadon sa
chatting yake sai faman murmurshi yake yana mamakin yanda ustaziya Halima ta iya tsara kalaman soyayya lalle zatayi dai dai da rayuwan sa

Ummi ceta turo kofan juyowa yayi yaga wane isheshen ne ya shigo masa bako Knocking

yana ganin Ummi ce yasaki murmurshi yace "Hajiya Ummi yanzu fa nake cewa zanje part din ku saboda Matawalle yace zai zo gaida Ummati na dan duk abokaina wanda bai zo yaga uwata ba bani bashi. "

zama Ummi tayi abakin gadon tace "AI son nata abaki ne inda da gaske kake son nata meya hana kaso jininta."

"haba Ummi ina son su mana yanzu nan fa muka gama chatting da Aunty Yusura ta bani Hajara da Ameer muka gaisa."

"meyasa baka son Ruwaida yanzu kwananta nawa a asibiti amma tunran daka kai ta kabar ta kazo baka koma ba gashi har gobe tafiyan ku ni banga kana wani shiri ba duk kabarwa daddyn ku aikin."

"Ummi tafiya kuma ina.?

"au ba kama san da tafiyan ba sabar baka damu ba to zaku fita da Ruwaida ne india."

"Ummi kuma aka bar Khalifa ya koma ba shine likita ba ai shi ya dace ya kaita."

"Kai da maka dace ba Kai zaka Kai ta dan Khalifa an masa kiran gaggawa yakoma amma zai sameku a can zai Kai wani abokin sa doctor zai duba mahaifan nata."

"gaskiya Ummi bani da Time kawai su tafi ko da Anas."

"Ismail ni kake cewa baka da lokacin aikin da na saka?

"sorry Ummi zanje."

Ismail baya son bacin ran Ummin sa yana son farin cikinta dan haka ya

amince badan zai iya tafiya da wanda yafi tsana a duniya ba

daga Ruwaida sai Kharajina sai Ismail suka tafi
(*INDIA*)

Ismail tunda ya kai su asbiti bai kara bita kan suba yariga yagama da biyan komai nasu

yasamu hotel yayi zaman sa dan shi jiran yaji ance Ruwa ta mutu kawai yake ayanda yaga tana jin jiki

Ummi kullum sai sun kira Idan ta tambayi Ismail suce yafita haka idan shi tafara kira yace yabar wajen su yanzu

An duba bakin Ruwaida sai da aka bata magani na sati tukun aka shiga aiki da ita ana zatawa aikin yayi kyu amma tayi rashin hak'oran gaba guda biyu saboda cire dadashin kasan hakorin da akayi dan yagama lalacewa sai gefen harsheta da aka dan yanke saboda rubewan wajen

Hamrah da Ayya ma sunzo
Amma sun koma

Mahaifa kuma shima wani kwararren Doc ne Khalifa yazo dashi a Germany amma magani kawai ya daura ta akai yace aiki bazai yuwu ba sai ta gama warkewa da cancer din za amata aiki amma magani zai hana ciwon cigaba

Affan da mommy da suka zo a lokacin jikin Ruwaida ya matsa sosai dan magani ya fara aiki kunsa ance ciwo shi yake fitar da ciwo wani irin ruwa ne me wari yake fitowa a gabanta ka kurajen bakin sun kara fursowa sai wari yake
Affan kuka sosai yake ya fara cewa

"mommy kiga yanda Ruwaida ta takoma mommy idan na rasa Ruwaida nima mutuwa zanyi."

Ruwaida da harshen ta yake nade ba daman tayi magana sai bin Affan da mommy sa taken da kallo hawayen bakin ciki Yana bin kumatunta

Affan da Mommy sa masu sonta ne sakani da Allah ta tsaya jiran wani Mall da bai san darajan ta ba inama zata warke ta samu dama bazata taba bari Affan ya wuce taba dubi yanda take cikin wannan halin amma basu gujeta ba duk da ba yau ta fara mamakin yanda Affan yake sonta ba amma yanzu ta gane Affan Ruwaida yake so ba kyanta ko wani abunta ba
Allah kasake bani dama zanyi amfani dashi ina ma zan warke na auri Affan

na nuna masa so

Jikin mommy ta fad'a tafara kuka ita ma mommy kukan ta fara
Tana lallashinta da zata warke kuma koda ancire mata mahaifa Affan zai zauna da ita

Affan da mommy ba karamin temako suka bawa su Ruwaida ba dan tattali da kulawa har aka cire mata bandage harshen ta

ta fara magana amma kadan kadan

Ummi ko sam hankalin bai kwanta da yanda Ismail yake tsula mata k'arya ba dan a k'allla zata kira su Ruwaida so 4 a rana amma kowane lokaci zancen dayane Yamall yafita

shima haka yace yanzu na barsu shiko nan ko awaya sai yayi kwana biyu bai kira Kharajina ba

Akwai ranan da yakira Kharajina tafita wayan yana kusa da Ruwaida dauka tayi cikin tsarkeken muryar tayi sallama

"what!! da kazamin bakin ki kika daumin waya"

 kafin ta ce wani Abu har yakashe

Ruwaida kuka ta fara dan duk wannan abin son Mall yana nan agefin zuciyar ta kawai Affan dan yana kyutata matane

Ummi takira Mall

tace "Ismail inason ka hadani da Ruwaida awayan ka yanzu hankalina ya kasa kwanciya da yanda kake kula dasu ni kuma ga Khareji ta shiga watan haifuwa ba daman na barta."

"OK Ummi."

Awaje mall ya tsaya yakira Kharajina
yace "kisa meni a waje."

rai ab'ace ya Kalli Kharajina yace" Ummi tana son cusa min wannan k'azantan Wllh wai fa yanzu kirana tayi wai na dauki waya ta nabawa wannan k'azaman zasuyi magana Wllh da nabata wayana kwara na bawa kuturwa tayi waya dashi

dan haka yanzu zankira Ummi ki karbi wayan kuyi magana a matsayin kece Ruwaida nake ga bazata gane ba ai muryar ku iri daya ne kika kuskura kika bani failure zaki rena kanki."
Yace tare da meka mata

"Hello Ummi ."

.tace cikin nok'e harshe kamar yanda Ruwaida take magana

"yawwa Ruwaida yayan naku yana kula daku yanda ya kamata ko."

"Eh Ummi."

"Masha Allah amma yanzu naji muryar naki Ya fara fitowa sosai ba kaman d'azu ba harshe ya bushe ne.?

"Eh Ummi da sauki."

"Alhamdulilah naji dadi Wllh inda danna min video call nasake gani."

"um um."

tace dan ta gigice sosai
Ismail Karban wayan yayi ya kashe kaba d'aya

yace
"naje duba kudin da akayi charging namu this week
Amma aka ce anbiya harda ragowan canji ma muke binsu waye
AFFAN SULEMAN TABAR.?

Kharajina tace "saurayin tane suka zoda mommy sa suna da kirki suna son Ruwaida irin son mamakin nan baka ga yanda suke kula damu ba."

Murmurshi yayi yace "Good yayi kyu ai dama irin su da suka san darajan ta suya kamata suyi zaman jinyanta ni gobe ina son zan wuce amma kar ki gayawa Ummi zata iya hanawa."

Ismail a Nigeria

duk kan su zaune a parlour Ummi

Ummi tace "ni har yanzu baka gaya min dalilin ka na barin Marar lafiya kazo ba."

"Ummi me amfanin zamana naga *kwarton* ta yabita har da uwar sa ni kuma zaman me zanyi bayan ga abinyi agabana."

Ummi da haushin Ismail Ya kaita wuya
tace "in ma daduron tane me yasa kazo baka sanar dani ba."

"Ummi yan gidan su Halima ne suka matsa na turo."

"katuro ayi me"

Yace "maganan aure mana za a tsayar."

Ummi tace "OK amma iyayen ku maza sunyi shawaran Kai da Sa adu tunda kune manya acikin gidan nan zaku zauna har anfara ginin daga acan filin bayan gidan Daddyn ku Idiris amma ina tsammanin bazai wuce part din Mace daya ba sai de idan karawa zakayi."

washe baki yayi yace nima nafi son zaman gida ba wani k'arawan da zanyi Mace daya ta isheni ai."

Murmurshin mugunta Ummi tayi
 tace "kenan baka bukatan HALIMA ko."

"bangane ba Ummi."

"Ai kai yanzu kana da aure tarewa kawai yarage wa matar ka
bayan tafinyan ku da kwana daya nasa an daura maka aure kai da Ruwaida dan maganan kana ba lalle ta rayu ba ya girgizani ina tsoron kar ta mutu ba aure a kanta shine na matsa aka daura auren."

bai yarda ba dan haka fuskan sa dauke da murmurshi ya juta ya Kalli Umman Ruwaida

yace "Ummatee wai ana irin wannan auren dama ko ba namiji kawai sai adaura masa aure."

Umma tace "Eh d'ana nide ba abinda Zance sai Allah yasan Ya albarka dan nayi murnan wannan had'in."

awani irin razane Mall ya mek'e yace "wai dama da gaske ne?

wllh da a aura min ita kwara an auramin Iya Ramatu"

Iya Ramata wata tsohuwar me aikin sune da ta tsufa aka hanata aiki amma tana gidan tazama kamar kakar su

dariya Ummi tayi tace "haba Samaila Iya Ramatu da nima tayi jika dani AI.....

da sauri ya katse Ummin

"Wllh kwara ita ni da ace wannan k'azantan Wllh kwara ku auramin gurguwa makahuwa kurma kuturwa
Ai koda mutuwan zatayi Wllh karuwa ba zata mutu min da aure ba gwara kuturwa wllh bat.....

"Ismail shiru yayi dalilin ganin yanda Umman Ruwaida ta dafe cikin ta da daya hannun ta daya kuma tana yarfashi

Ummi ko cewa tayi "Ismail kana son kashenin yar uwa ko nashiga ukku ni Aishatu mezan ga Khareji jine nefa ya tsunko miki.....

Tofa yaya Affan da mommy zasuji batun auren nan

Mall fa

Wllh nikam yanzu Team *AFFAN* 😭

*B Jattko**AMFANIN SOYAYYA*
(aure)

NA

BATUL ADAM JATTKO
ASHBAT

Atemaka min da
Cigaban Wani novel daga pg 17

Na manta sunan sa

Wanda wani mutum yake auran mata biyu amma bai san biyu Ya aura ba
Yana zaune da matan biyu a gida daya amma bai sani ba shi a daukan sa da daya yake zaune *kuma dukan su biyun suna haifuwa*
amma Bai sani ba dan shi d'aya ya aura

Sunan mutumin Mukaddam
please
AMIN TEMAKO
😭😭

Sis
sunan sa
amfanin soyayya

shikiman Jattko

□□
Kai sis ina jin dadin irin wannan comment din naku □□
Jattkon ku

Please wanda suka min magana ta private suka ga banyi Ripley ba Wllh network ne yahana yazo amma ni naga tsakon ku

KAINUWA WRITERS ASSOCIATION

17

Umma rik'e Ummi tayi gam tana wani irin nishi sai ka sunkucecen Yaro yafado sai kuka yake Ummi tsabar murna gigicewa tayi

ta kalli Mall da sai raba ido yake tace "ai sai kaje ka kira min Umman Nafi

Umman Sall ce ta shigo tana tafa hannu
"kai kai "HAJIYA Ruwaiya ya haka kin bar yaro yana yawo a katsan style baza ki yanke cibiya ki dauke shiba da sanyin nan."

"Wllh yaya Turai rasa abin yi nayi duk na gigice memo reza."

cikin k'an kanin lokaci aka wanki Hjy Kharaji da san talelen dan ta mekama da Muk'adda sak

Mall ne ya dauki yaron sai addua yake masa Maman Farida ce tace "Mall ka makale yaro kawoshi nagashi

Murmurshi yayi yace "Mama hudduba fa na masa sunann sa ABDULRAHMAN amma Imran za ace masa ina son sunan ."

yayi maganan Yana mekawa Mama yaron

Ummi tace jiwani iko sai kace d'an sa."

dariya Mama tayi tace" ai ni Mall mamaki yake bani yanda yake jida Ummatin nan tashi yakoma kamar ba sojan da yake mana muzurai ba har yazauna a parlourn da mutane suke ana fira da shi ai abune dako a kuruciyar bai yiba."

Murmurshi Mall yayi yamek'e ya taka har inda Umma take yace" Hajiya Ummatee mekike bukata."

murmurshi Umman Ruwaida tayi tace Kai nake son kani d'ana."

tameke sukayi kanyan bedroom din Ummi

sai da tajira yashiga ta rufe kofan har da key

suka zauna abakin gado

"Ismail zanmaka tambaya amma sai kamin alkawarin gaskiya zaka fad'a min duk d'acin sa."

"Ummati dan baki san halina bane ni bansan karya da canza zance ba bana Iya yinshi tun ina yaro duk abin dana fada a gida ba amusa min gaskiya nake fada duk d'acin sa kuma ni Kai tsaye nake Abu ba kwane kwane

ko me kika bukata inde nasani gaskiyar zan gaya miki."

"ina son ka gayamin gaskiya akan yaya rayuwan k'anwarka Ruwaida ya kasance bayan bana nan."?

"Ummati bana son kina damun kanki da rayuwan Ruwaida bata san kanta ba UMMA Ruwaida ta bata rayuwanta ta bata nawa tunda nafara ganin Ruwaida sonta da kaunata yaso yamin illah aranan da muka hadu da ita aranan nake shirin barin kasan nan zuwa American inda nake koyan aiki har nayi sallah ma da gida dama ta kaduna zan tashi shine na tsaya a wajen wani abokina dan gidan governorn kaduna anan muka hadu da Ruwaida muna rabuwa na tashi sai da naje America na dauki wayana da sunan kiran Ruwaida narasa number nakira yarona da na bawa yanin saving din number sai yake gayamin nayi hakuri memakon yayi saving yayi mistake yayi delete yaji tsoron gaya min ne a lokacin

nasa Matawale ya nemo min ita yace wai ankoreta a gidan to dama cemin akayi kanwar matar gidan ce nasha wahala har na kasa jurewa nazo dan nemanta

da kaina naje gidan har Abban ta Mudda nagani ya cemin shi bai ma santa ba ya manta haka matar sa ma shine na ke ta wahalan neman ta kwasam na tsinceta da wani shiga

daga nan yakwashe duk tarishin Ruwaida wanda aka boyewa Umma yagaya mata

yana kaiwa karshe ya dunkule hannunsa ya naushi tafin daya hannun idon so yayi wani irin ja ina ma zai samu yayi kuka da yaji dadi

Umma jawo shi tayi ta daura kansa akan cinyar ta tana shafawa ita ma hawaye ne yake zubo mata

Sai a sannan Mall yasamu hawaye yazubo masa wanda wannan kukan rahma ne a wajen sa cikin kuka ya fara magana

"Umma meyasa Ruwaida tamin haka meyasa ta dasa min sonta da farko kuma daga karshe ta dasa min k'inta Wllh Umma ko sunan Ruwaida bana son ji auren ta da Ummi tace an dauramin idan da gaskene yazanyi Umma ki temakeni ki shawomin kan Ummi Wllh bazan iya rayuwa da ita ba."

d'ago kansa Umma tayi suna fuskantan juna tace " Ismail kana son nacewa Yaya tasa a raba auren ku da Ruwaida kenan ko?.

Yace
"Eh."

"OK amma baka ganin Kai amatsayin kana dan uwan ta baka zauna da ita ba balle bare."?

"Umma acikin yan iskanta zata samu Wanda yayi daidai da rayuwanta ni bazan iya hada ko zaman gida daya da ita ba."

"shikenan kabar komai a hannuna zan san yanda zanyi bazata tare ba amma kayi hakuri mugama babban case din da yake tsakanin mu da Mukaddam kafin mudawo kanku."

"OK my mommy."

Borno

Mama Kangiram daky'ar tayar da aka sasanta ta da Duno sai da Ayya tayi ta sa baki Ayya tasa ansake gina musu gidan dukiya kuma bata dan kawa Duno gaba daya ba amma ta bashi babban mukami

shiriye shirye bikin su sai kabatowa yake

shiko Duno yagama zama abin tausayi kunya duniya yak'are masa Mama kam tunda asiri yatuno bata kulasa kullu cikin kuka Mama take idan ta tuno wai mijin ta yayi taraiya da y'arta sannan ya zamar da k'awar yarta tamkar matar sa bugu da K'ari kuma wai yaranta sun aure juna har da yara a tsakani anya aduniya akwai wanda yakaita jin kuncin duniyar nan kuwa
Allah kayafe min so daya nayi zina amma yamin yad'on da yafi karfin hankalina

zaune suke a
Dining area Duno kunyar Ayya ya hanasa sakewa dan ko ido baya bari su hada da Ayya da Mama yarame gama daya ga ciwon zuciya yayi mugum kamasa aikin ma yana zuwane saboda yasan zai nisan ta kansa da ganin Ayya da Mama

wayan sa dayake hannun Barrat ne yayi k'ara tamek'a masa karba yayi ya kara akunnu

"Innalilashi
to Alhamdulilah Allah nagode maka dawanan jarabawan kaya femin sauran zunubai na to nagode."

yakashe wayan tare da sakin kuka

Mama ta ajiye spoon hannun ta ta kalleshi tace
"lafiya.?

numfasawa yayi yace "Mudu yaje yayi shaye shayen sa ya dauki jigi daga shi sai Amina da yaran su acikin jirgin yakife kuma yakama da wuta ko tokan su basu samu sun iba ba Amar abokin sane ya kirani."

Kuka Mama tasa "yanzu mezan cewa wannan mutuwan Amina da Amudu sallah bai damesu ba ko nace basayi ka sun zauna cikin haramci

ga Balkisu ta haukace a shaye shaye ga Kai abinda kayi har na koma ga Allah bazan manta ba duk wannan abin yafaru ne dalilin zina da nayi so daya tak a rayuwata Allah kayafenin

shima Duno cikin kuka yace "bake kika jawo haka ba nine ai ga yar zinan nan ita ce take amfanan mu namu na hallak din sun b'aci feye da yanda nake son Ayyaram ta b'aci gashi ita ta zama shiryeyiya take amfanan mu

duk da mummunan halinda na jefata har da haifuwan shege nasan duk da ita tace ta yafemin hakkin ta dana Barrat bazai barni ba

Itama Ayya kuka tasa sosai dan taji mutuwan yan uwata

dangi ma na kusa aka gayawa mutuwan bawani zaman makoki da akayi dan jikin alh Duno ya matsa yakai shi da kwanciyar asbiti ana shirin fita dashi yace ga garinku Ayya da Mama sunyi kukan rashin sa

Adamawa Yola

Nura

Nura Saura kwanaki uku yarage wa adin da aka yanke masa yacika idan bai kawo kudin da ya sata ba zai ziyarci prison

abin duniya Ya isheshi sai yatashi ko 5 bashi dashi ajikin sa dama gidan su dashi suka dogara bawani me sana a dan dama basuda sanar da yawuce k'ira amma tunda yasamu kudi ya hana kowa k'ira ya dauki nauyin su amma yanzu sauran mutan gida sun koma k'iran su
kuma ko sile ba me bashi dama dama ma mamar sa

tunani yayi anya bazai fito ya fadi abin da yayiwa Hamrah ba ko zata temaka masa

wajen Baba Haruna yaje yakaranta masa komai daga farkon rayuwan har karshe

girgiza Kai Baba Haruna yayi yace "nidama nasan ba kada gaskiya nun alokacin na fad'a ai amma ganin yanda Kabiru ya Dauki zafi yasa nabar Hamrah ta tafi

Nura kai mugune makiri ka zalici iyalin Kabiru
Mukan mu ka yaudaremu Nura alokacin da ma mahaifin mu zai rasu kama hannuna yayi ya dan k'amin Kabiru yace yasan ni kad'ai ne meson Kabiru bana nuna masa y'an ubance narike shi amana amma harda ni a Koran Kabiru a gidan uban sa naci amanan mahaifina
Nura ka cuceni gashinan zaka girbi abinda kashuka

nasan bayanda za ayi su yafe maka nide bani aciki zanjena nemi gafaran abinda nayiwa dan uwana kawai."

Kuka sosai Nura ya fara yana rok'on sa dan yasan shi kadai ne yake da d'an mutumci a idon family Kabiru

Baba Haruna yace "ai sai
ka tara sauran iyayen ka mata da maza ka karanto musu komai kamar yanda kayi a randa kakawo min results din cikin Hamrah

haka ko akayi a babban parlour da Nura ya gina musu na family meeting duk da bawani k'ayatacce bane amma an malale shi da carpet sai setting din kujeru guda 2

Salatin su kawai kake ji da kukan Baban Nura da mamar sa

Baba Habu yace"ni tsorona hakkin yaran nan ba Hamrah ba hatta Juwairiya bamu bari ba muke ta sawa ana fasa auren ta gashi yanzu abin ya zame musu hassada ga me rabo yanda naji a anguwa ana zuzuta gidan Kabiru yasa naje wucewa ta kofan gidan naje na dawo yafe so 10 gidan kamar gidan gomna."

baba Habibu ma yace "ashe kaima kayi ni har lek'awa nayi megadi yace wajen wa nazo nace kallo kawai nazo yace na bar wajen."

Haka suma matan kowa fadan yanda su Hamrah suka daukaka sukeyi

haka suka iba kwansu da kwarkwatar su suka tafi gidan Baba Kabiru kurma

Allah ya temake su megadi Yana sallah suka tura get suka shige

Wassileem suka fara gani a saman mota yana waya da sauri Kamilu dan gidan Baba Habu yayi inda yake

"Kai Kai wass kai kazama haka kazama kamar wani bature kazama k'ato haka kasamu duniya."

ayangace Wassileem ya sauke wayan yafara bin su da kallon baku kai masu aikin mu ba
san nan yasauke idon sa akan
Kamalu

"Eh nine WASSILEEM KABIR SANKIRA
d'an gadon talauci da kurmanta."

"haba wassileem ai tunda muka taka muka zo komai yawuce ai."

Wasileem ya Kalli Baba Hamza dayayi maganan
Yace
"Eh komai yawuce kufita kutafi mun gode dan Wllh ina da cutan tsantsani idan naci gaba da ganin ku zan iya amayar da abincin da naci ku b'ace mana."

Baba Hakuna yace Muhammadu mu kake gayawa haka."

durowa yayi a saman motan Yana toshe hanci yace "Baba Haruna kana da sauran mutumci a idona karka ka bari ya zube
 katar kata tar kacen ka kufita mana agid.....

wani tsawa Hamrah da tun shigo wansu tana sama tana kallonsu tayi

"Wasileem baka da hankali ko y'an uwan mahaifin namu Kake yiwa haka muna da wanda yafisu ne".

Wassileem da yanzu ganin kansa yake kamar wani yayan ta dan yanda yacika ido irin mazan nan ne masu k'iran zaki gashi zanbet yake a tsaye kamar yayi k'anwa na 3 da ita a idon

wani kallo yamata yace "ai sai ki samesu a waje dan yanzu zansa ayi waje dasu."

da gudu Hamrah tayi cikin gida dan tasan zai iya

Baban su ta jawo da sauri dan ba iya yi masa Magana zatayi ba

yana kanin su Kabiru bawan Allah yafara washe baki duk yadin ga mek'amusu hannu suna gaisawa Yana nuna alamun yaji dadi dan Yana son danginsa amma Yana zuwa kan Nura ya shakunu Yana ingizashi yafeta da k'ar Baba Haruna ya hana suka shiga ciki duka

Wassilim yace "yanzu ke da hankalinki kike son k'ara kawo mana tar kacen nan ko.?

"Haba wassileem bamu da danginda yawuce su fa bakaji ance da uba ake ado ba shikansa Baba sune gatansa fa."

"tsaki yayi yabude mota yashiga yamata key ya fusga da karfi

ita ma komawa ciki tayi

Sosai Nura yake kuma agaban Hamrah

"YaNura ba nace na yafe maka ba."

"nagode Hamrah amma kisani Wllh nima bansan na ginu da sonki da yawa ba saida narasa ki ashe kudi basa maganin so."

Sadiya tace "Hamrah jin abinda Abban Khairat yamiki naso fita a gidan sa sai de yanda muka tara zuria nasan fitan ba mafita bane dan Allah ki yafe masa ko dan yaruwan yaran mu yayi kyau."

"nayafe fa Sadiya."

Nura yace "maganan kudin bank fa."

Hamrah tace
"kudin yana wajen accounter OK dina yake jira yashigar da kudin da sa hannun ka."

washe baki yayi yace nagode yar uwa".

to maganan aikina da kud'in na cikin account fa."

"kallon sa Hamrah tayi tace babu su kud'i na zuba a abubun barayu aikin ka kuma tunda ba kada takardu baza ka samu ba."

atsoroce yace "kina nufin document dina bazasu dawo ba dan Allah Hamrah ki temakeni kibani takadduna."

"Wllh Ya Nura babu su muna kar bosu Ruwaida ta cilla masa wuta yayi kurmu ."

.wani irin kuka Nura yasa

Mamar sa tace "Kai ka godewa Allah mana da baza a kai ka gidan yari ba."

Hamrah tace "kuma zanci gaba da daukan duk nauyin gidan kowa yayi list din abinda yake kashewa a wata yaran duk zan canza musu makaranta sannan wanda suka gama sukawo takardun su nace gaba zasu cigaba na aiki zan sa anemo musu."

duk godiya suka shiga yi mata

shide Nuraddin kuka kawai yake dan yasan bashida wani amfani dunta ko messenger bazai yuwu abashi ba a wannan zamanin bashida ko shidan primary school

bayan kwana biyu Nura yasake zuwa har da kukansa Hamrah ta fasa auren Sahal ta aure sa

"dan Allah Hamrah ki sani ke nafara so arayuwa wllh bazan kuma mai maita lefina ba."

Murmurshi tayi tafara masa wak'a

na aminta da Kaii Nurah na yarda zaka rik'eni amana in angano wata za aga zahra AISHA Humaira ce ta Nura

katuno wannan Film din shima yace amana ai inaga abin masu irin sunan ku yabi

Kuka ya fara" nasan kinfi ajina Hamrah amma kisani Wllh duk abinda ya sameni kece tsila arasin kine

Kuma Wllh Wllh inde ni Nura ina numbashi bazan taba barinki ki zauna lafiya

ba ko agidan majalisan d'inkin duniya ne balle wani d'an gidan tsohon matemakin shugaban k'asan Nigeria Sa adun banza."

Hamrah tace
"haka kace."

"haka nace kuma zan aikata."

"Bissmillah."

juyawa yayi yafita

Bayan wata ukku anyi auren Ayya da grema bawani biki da akayi saboda mutuwar Duno amarya ta tare sai kuma koya tsarin zaman zai kasance."

Egypt

a Egypt kuwa Ummusulem ta haifu d'anta namiji Mukddam yasa sunan shugaman kasa babban aminin sa Zahkar

Mudda zaune cikin yaran sa dama idan yana gari dauke yaran Kharajina ake sai yatafi a kawosu

"haba yusura ni ayau nake son tafiya da matata nanunawa duniya
 da dangina nafito nanuna Ahlan da Sahlan ma yaranane zan fito na fadi gaskiya abin da yafuru tsakani na da Ummusulem nasan Hajja da malama zasu fashimceni kuma na gaya mata tayi sa ar abokiyar zama bazata mata muguntan da wancen kishiyar ta mata ta haukata ta ba

tana da sani sosai ga shikkimar malinta
 akwai wani aure da nayi
Wllh ita malama ita tasani nayi."

Yusura tace "haba kataba aure Kennan. "?
"

"Eh amma matar ta rasu."

Yusura tace
Ayya Allah yajikanta ya sunanta?

da sauri Ummusulem tace Kharajina."

Atsorace ya kalketa yace "waya gaya miki."?

Murmurshi tayi tace "kamanta kullum kana cewa itan muka rufe ido Kharajina nake komawa ."

Shima murmurshi yayi yace "haka nefa."

yanzu de goben tafiyan Yana nan ko."

Ummusulem tace "eh amma akano wajen dangina zan fara sauka tukun".

"OK nima nafi son nafara ganawa da dangin naki tukun

washe gari suka tattara suka dawo

Agidan su Mall suka sauka
Cikin mamaki Mukaddam yace "ai wannan GIda Haruna walwalane .?

Ummusule tace "eh ai yayata ce take auren Wakili walwalah

Tofa wannan babban magana ne dan nesa tazo kusa abinda kuke jira yazo amma kafin nan bari nalek'a wajen Ruwaida

jiki yayi sauki har ansa ranan aikin mahaifan ta

Hamrah ce takai mata ziyara ita da Juwa da Wassileem

Suna zaune suna fira da ita da Kharajina da Ruwaida Juwa da Wasileem sun fita da Affan

Mommy Affan ta koma amma yanda taken kiran Ruwaida da kula da ita ko su ummi ba sayi

Ruwaida "tace sis yana ga duk kin rame ne."

Kuka Hamrah ta fashe dashi tace "sis dole na rame Wllh ina gani mu kuma a duniya irin k'addaran mu Kennan inaga bazamu taba samun jin dadi ba."

wawulun bakin ta Ruwaida ta bude tace "sis zaki sa zuciyata ta buga meyake faruwa ki gaya min."

Hamrah tace da Aunty Ayya tace kar mu gaya miki agani na rashin gaya mikin bashi da wani amfani

Ruwaida muncuci kanmu ba muyiwa kan mu adalciba gashi mundena zina zina bata dena bin muba

Ayya da zasuyi aure ita ta Grema sunje kwaji akace tana da ciwon hanta wanda ana daukan sa sai da ta gaya min natuno mata ajikin Alhaji Bala Oliya ta iba kin san ana daukan sa ta hanya hada numfashi ko yayu tatta a saduwa ana dauka amma dayake Grema Yana sonta ya rufe abin akayi auren amma tunda akayi aure ko hannun ta bai rike ba yanzu haka ita nazo dubawa tana nan india tana karban magani."

wani irin kuka Ruwaida tasa tamek'e tace "ki kai ni wajenta dan Allah."

Hannu ta Hamrah ta kama tace "sis nima ina da nawa
matsala Ruwaida a yanzu ina shirin fasa auren Sahal

"dan me meyafaru?

share hawayenta Hamrah tayi tace tunda aka yanke auren mu Yasall bai bari na zauna lafiya ba akullum cikin zargina yake Abu k'adan zai hau gaya min maganganu yana min masifa
bayan ya kwace wayan hannun na
sabon da yabani
yaje yayi setting number nada nasa idan aka kirani shiyake rigani jin me za acemin shine muna waya da khaleel Dan gidan Baba Haruna yake gaya min yanda Nura yake haukan shi yadawo shi zai aureni

A ranan baki ga cin mutumcin da yamin ba
Aure da zargi matsalane kuma
anyi anyi ayi auren idan nashiga daga gidan sai na rufe duk wani hanyan da zai zargeni idan muna kusa da juna

amma yan gidan su sunce da auren Ya mall za ahad'a
Ita kuma Ummi ta kafe Mall bazaiyi aure ba sai kin tare da ganan ayi na wanda yake so din".

arazane Ruwaida tace ban gane sai na tare?

cikin mamaki Hamrah ta kalleta

Amma kafin tayi magana

Kharajina tace "ah ah tana nufin sai kin warke kintare gida ne ai ."

Tayi maganan tanayiwa Hamrah kallon zakiyi tabar gaza

Ita ma Hamrah sai asan nan ta tuno ashefa Ruwaida bata san ita matar Mall bace

"Ruwaida tace ni tashi ki kai ni naga Aunty Ayya
Inban da abin Ummi ni me gamina da wani auren Mall yayi mana ko ina garin ma bazan je wajen bikin ba

Tofa ya ruwaida zata yi idan tasan ita matar mall ce
affan fa😭

YA Mukaddam zaiyi idan yashiga yaga Khajina Ya malama zataji idan taga mukaddam da tarin yara da mata buyu

Wannan rikicin babbane Anzu wajen cakwaciyar fa

Ya batun nura na sai yaga bayan auren Hamrah

Kar ku damu da yawan post ingantacen labari sai da nazari dan sanu sanu bata hana zuwa ina jin dadin comment dinku

Amfanin soyayya yanzu aka fara ♀

*B JATTKO**AMFANIN SOYAYYA*
aure

NA

BATUL ADAM JATTKO
ASHBAT

Sis dan Allah kuyi hakuri da rashin amsa muku comment Wllh bani da network ne amma ni ina ganin duk comment din ku kuma duk group dinda nake ciki idan basu ga posting dina ba Wllh network ne ya hana yashigo amma ni hadawa nake nayi make duka Nagode

Musamman wanda suka min magana ta private Wllh na muku Ripley bai zoba ne kumin hakuri dan naga kunfusata sosai

kainuwa asso

18

Ayya nannun Ruwaida da Hamrah ta kama cikin mawuyacin hali
tace "Hamrah banace kar ki gayawa Ruwaida halin da nake ciki ba ita da bata da lafiya

Sis kuyafe min lefin da nayi muku azaman mu
sis na baku amanan Barrat duk da ba kwaina bace ni na kyankyasheta na haifeta da cikina shari a ta bani ita dan haka y'ata ce
na baku amanan ta

Ruwaida kiyi hakuri a duk halinda kika tsinci kanki a gidan auren ki da ya Mall wataran zai soki

dan Allah sis kudin ga sani cikin addua ku bani da wanda ya fiku ga Mamata zuciyarta ta buga bata san wanda yake kanta ba nasan Mama bazata yaru ba ko mata rasu aka boyemin dan nafi sati ban ganta ba bayan tare aka kawomu

Na raba dukiya na gida 5 daya nakune daya na Barrat daya akai gidan marayu daya dangin su Mama daya Grema

Barrat amanan ku Ruwaida
Kumin addua bani da gowa sai ku.....

cikin kuka Ruwaida tace "dama haka jikin ki yake ba agaya min ba

Aunty Ayya insha Allah bazaki mutu ba zaki tashi kamar yanda nima nasamu

lafiya.....

wani irin tari Ayya tafara saiga aman jini ta hanci ta baki

Da gudu doctor suka shigo dan naura yanuna musu komai shima Grema da gudu yashigo amma a bakin kofan ya kafe kamar wanda aka dasa shi baki kawai yabude yake ganin yanda ran Ayya ke son fita duk da danna mata kirji da agajin da doctor suke badawa
Ayya tana rike da hannun Ruwaida anyi anyi ankasa kwacewa har saida rai yayi halinsa

Allahukbar

atare Ruwaida da Hamrah suka zube a sume

dau kansu akayi aka fita dasu

Grema a hankani yake takawa har inda gawan Ayya yake

ahankali yaja ya bude ta "dagaske AISHA kintafi ki tashi mu rayu tare matata Aisha haka zakimin dafe kirjin sa yayi yaja wani irin numfashi yazube sumeme
to yaza ayi da abinda yake
(RUBUTACCI AL AMARI
GARKUWA TA)

ahankali take bude ido har ta sauke idon ta akan Affan kanta taji ya mata nauyi bin d'akin tayi da kallo tabbas ba d'akin ta bane wani k'ara ta kwala tare da mekewa tsaye

Affan yarik'e mata Hannu yana "please my love ki nayin addua."

"dan Allah Affan kar ka boyemin da gaske Ayya ta mutu."

" Kharajina ce tace dan Allah ki nusu sis duk merai bai wuce haka ba Ayya ta tafi meja da ikon Ta ala ne zaiyi kuka
Yau darin Alhamins ne gashi ta mutu da kalman shahada,
 addua yaka mata kumata idan son nata kukeyi ."

"Affan ka kaini wajen ta kaji."

Affan yace "sorry my love Wllh antafi da ita yanzu ina gama Sun tashi
Hamrah tariga ki far fadowa tare suka tafi
Sannan itama Maman Ayya ta rasu haka Allah Ya kaddara rana daya zasu

amsa kiran ubangiji
za ayi musu sutura a meduguri."

Ruwaida tace "wlllh bazan zauna ba sai ayi suturan Ayya dani
ganin tana Abu kamar bata cikin hankalinta ne yasa Affan yace "to mutafi inyaso mucewa doctor zamuje mudawo ko nasan yanzu basu tashi ba

Airport
hakan ko akayi basu tashin ba tare suka kai gawan kuka da damuwa awajen Hamrah da Ruwaida
ko magana sun kasa yi sai bin kowa da kallo kawai

Gidan walwala
Ummi runguman Ummusulem tayi na murna kamar da gaske yar uwar tace

tace Ummusulem Ashe zan ganki keda akace mana kin mutu bakin cikin y'arki ta haifi cikin shege kuma ta daura miki tace ke kika haifu yasa zuciyarki ta buga kin mutu.?

Murmurshi Ummusulem tayi tace"yaya makircin kishiyane nice na haifu ba Ruwaidan bace ina haifuwa ta haukatani tace Ruwaida ce ta haifu ni na mutu suka samu wani gawan akayi masa sutura ni kuma Aminu ya kai ni can wani jejin kinga wanda ya tsinceni nan tanuna Mukaddam da yasaki baki cikin mamaki
yana kallon gashi matar tayi kama da Kharajina

Ummi tayi salati tace ikon Allah duk tsoron Allah rin na Malama ta iya yin haka."

Mukaddam kam abin yayi mugun daure masa Kai gaban sa yaji Yana faduwa to meye haka malama Ruwaida
YA abin yake mishi kama da Storyn family sa
Saurin girgiza Kai yayi yace malama bazata tabayin haka ba kuma ai ummusulem ba Kharajina bace lefina ban taba tambayan Ummusulem ya rayuwanta yakasan ce a baya ba

Ummi ceta katse masa tunani da cewa "to ummusulem ai wannan Mai kwano ne Alhaji Mukaddam."

"Eh shine mijina."

"ok Alhaji na kira mazan gidan yanzu zasu zo dan sunfita..

Kafin ta rufe maki sai ga Alh Haruna da Alh Ideeris da Prof Wakili sun shego."

sai Mall dasu Anas

Alh Mudda dama akokaine da Haruna sai adawan siyasa sosai aka gaisa ya gabatar da kansa amatsayin Mijin Ummusulem

Godiya suka shiga yimasa kamar gaske tare
su kaci abinci duk mazan a dining Area sai wani girmama Mukaddam suke sai bayan ishai

Mukaddam yatashi tafiya kaduna amma Ummusulem ta hana tace yabari goben sa wuce tare
da dare yayi zai tafi gidan sa na cikin Kano tace a a ita de anan zasu kwana baga part nan an ware musu ba

Murmurshi yayi yace "mata mata masu mulki inban da ku wazaice babban mutum kamar ni me kwano na kwana gidan mutane nayi yaya da security dina
Kinsan ni waye a Nigeria kuwa."?

zunburo baki gaba tayi tace " niko nasan waye Mudda amma yau agidan yayata zamu kwana
 bawani security sunfi matar ka son kane ".

Murmurshi yayi yace" yanda kike son haka za ayi

Yace "Amma tambaya ne fal abakina yau?."

tace "wane tambaya.?

"game da abinda naji da zu game da rayuwanki zaki min karin bayani."

Tace "gaskiya da gajiya a jikina bari na karbo Zahkar mu kwata sai
 da safe zan baka amsan
Amma kafin na tafi sai kagama komai nashirin ka dan yau aduhu nake so zan Kashe tuwan."

washe baki yayi dan yayi missing din yi aduhu kullu tace ita ah ah

"to to ai nagama jeki dauko sa karki jima."

Sai da takashe wutan tukun tafita

ta bangaren Ummi sun gama komai na gabatar da Kharajina Yusura ma tabiyo bayan su da yaran Kharajina

"Wllh Ummusul dita ke ta daman ce acikin duhu Allah yamiki baiwa biyu amma na duhu yafi dadi Kai k'irjin ki ma aduhu k'ara girma suke laushin fatan ki da komai naki
kina tuno min da Kharajina ta...

"Kai wannan Kharajinan da take bakin ka kullum Yau har kama da ita a zashiri zanyi

wani murya da ya kid'ima Mukaddam yadoki dodon kunnnen sa dama bata taba magana ba sai yau

arazane yace "muryar ma na Kharajina ne."

Kharajina tace "har kaman bari kaga."

Tana gama maganan taja wutan ta kunna dakin ya kauraye da haske

"murmurshi tayi tace "yade ko ba muyi kaman bane ?

Mukaddam dafa bango yayi yana kokarin shigewa ciki sai zare ido yake

atsora ce ya fara magana "dan Allah ummusulem kiyi hakuri ki koma yanda kike Wllh ban san aljanun da suka samiki hauka basu fita ba Ashe su suke juya ki kike komawa Kharajina a duhu."

Murmurshi Umman Ruwaida tayi tace "shiga kayi wanka kafito kasa kayanka sai ayi maganan ko."

da sauri ya kwashi kayan sa yayi hanyan toilet ya rofo kofan har da key

dariya abin yabawa Umma ashe maza ma suna tsoro

Tashi ita ma tayi tashiga daya bedroom din tashiga bathroom din ciki ta shirya tafito

Har lokacin Mukaddam bai fito ba

Parlour ta fito inda ummusulem take tace "Ummu Ina gafa Sai kin shiga kin fito da Mijin ki fa".
ta kwashe yanda sukayi ta gaya mata

dariya ita ma tayi tace "to kije ki kira su yayan kafin na fito dashi."

"haba habibi ka bude kofan mana."

"kin koma ummusulem dinki ko.?

Tana danne dariyar ta tace "Eh nakoma."

Fitowa yayi yana rarraba ido

yace "ai ke aikin danye ne baki warke ba aljanun basu bar jikin kiba."

tace "ras nake sai de falawan matar kace take maka gizau."

Muje falo ta kama hannu sa Mudda har yanzu a tsorace yake

Suna fitowa parlour yaci karo da duka mutanen gidan cikin mamaki yake binsu da kallo to meyakawo su bangaren da suka sauke su a wannan daren amma kawai saiya wayince

yayi murmurshi yace "walwala na talakawa sai kayi."

Murmurshi Alh Haruna yayi yace "in boka auta ya mutu ko."?

atsorce Mudda ya kalleshi amma dayake dan duniya ne kawai ya wayinci dacewa
"waye kuma boka auta."

Alha Haruna yace "duk ba wannan bane dalilin taron mu anan

Mukaddam kasan wannan yanuna masa?
Kharajina

Idon sane yasake sauka akanta arazane yameke

"wai me yake faruwa ne."?

Aminu ne yashigo yana cewa "Sir al kairi ne yake shirin faruwa wannan da kake gani ba kowa bace illah Khrajinan ka uwar yaran ka ba mutuwa tayi ba

makircin mune dan bazan cire kai na aciki ba amma banyi da son raina ba sai dan ina gudun tuggun da malama zata hada min awajen ka

Daga nan ya kwashe komai ya gayawa Mudda

Da babban sheda wato ashe yayi video komai na kulle kulle malama tunda ga ranan ta tafara har zuwa yanzu

dafe gansa Mudda yayi wasu abubuwa ne suke dawo masa wanda suke kara gaskanta abin da Aminu ya nuna masa

Kansa ya dafe Yana juyawa

Yace " yanzu ina Abdallah ina Ruwaida Ahlan da Sahlan yaran sunna ne da Kharajina nasa mesu ina Amira da Ameer din ina Abdulrahman din duk aka meko masa
Rumgume Abdallah yayi Yana Kuka yara har 4 nawa bansan da zaman su ba gashi duk masu kama dadi

da karfi yace
"MALAMA

AUTA

KAMAL

DOCTOR HABIB

TABAWA

dama kune makiyana a guniya za.....

salati da gigicewa da Sahal yayi ne ya katse Mukaddam
kowa yashiga tambayar Sahal meya faru?

Allah yayiwa Ayyaram k'awar su Hamrah rasuwa...

Dak suka fara salati dan sunsan Ayya da halayen ta masu kyu adan zaman da tayi dasu

Hatta oga Mall yaji mutuwan

Wayyo RIP AYYA 😭😭😭😭

Dalilin haka nima na dan dakata

Dama nadan bakune saboda kuci dariyan Mudda da Aljana Kharajina

*B JATTKO**AMFANI SOYAYYA*
aure

NA

BATUL ADAM JATTKO

Kainuwa asso

19

Mukaddam ta yaran sa da matar sa yake
su kuma mutanen gidan kowa jimamin mutuwan Ayya yake

da gudu Farida tashigo falon tana kuka" Ummi wai da gaske Aunty Ayyan su Ruwaida ta k
mutu Wllh yanzu nagani an daura pic dinta a facebook wai ta rasu dama ina ta kiran wayan ta kwana biyu baya shiga."

shima Mukaddam sai asannan yagane wa ake magana duk daba alkairi ya hadasu ba yaji mutuwan ta

Kowa da jimamin abin ya kwanta baye yan matan gidan da sunyi zaman dadi da Ayya

bayan kowa ya fita anbar Mukaddam da iyalin shi ya kasa sauk'e Abdulrahman a cinyan sa sai faman lallashin Abdallah da yaki dena kukan mutuwar Ayya yake

"haba Abdallah kayi hakuri ba ita ta rasu ba wata ce daban."
inji Mukaddam

Abdallah yace "itace mana ai YaSall aka gayawa kuma Aunty Farida ma gashi tace ta gani a facebook shikenan nida Barrat mun sake zama shegu..

atsorace daga Umma har Abban suka kalle shi

Idon Mudda ne yaciko da kwallah yace "waye ya taba ce maka shige.?

"a school dinmu ake gaya mana nida Barrat tunda bamu da Baba wai mu shegune mu k'azanta ne basa cin abincin mu wai mu y'ay'an yan ukku balai ne yanzu gashi mamar muma ta rasu Aunty Ruwaida batanan Aunty Hamrah bata nan
to ina Barrat din?."

Kuka yasake sawa

shima Mudda kuka yasa yasake runguman Abdallah

"nine Baban ka Kai d'anane."

Abdallah ya dago Kai ya Kalli Mukaddam
yace " moomi Ayya matar kace.?

Tambayan yabasu mamaki amma dayake yaran yanzu sunsan komai amma da mamaki Yaro dan shekara 6 kamar wannan har yasan haka

Mudda ya nuna Umma da ummusulem yace "ah ah kaga matana kuma kaga wannan itace mamar ka yanuna Umma."

"ah ah ni Moomin Ayya ce mamana."

girgiza kansa yayi yace "malama kin cuceni cuta ta har abada."
Umma tace "ai bawani abu bane dan Abdallah yace Ayya ce mamar sa kaman ta a labarin da aka baka yanzu Ayya ita ta shayar dashi kuma ai uwace tunda ta shayar dashi
sai de nace Allah yaji k'an Ashsha yaba mu ikon rike amanan y'arta Barrar."

"Kharajina ki yafemin wasarere danayi da rayuwan ki keda yaran ki saboda neman abin duniya gashi akan sa aka cutar min da iyali Kharajina kinyi hauka kinci abincin bola kin kwana a jeji kinyi yawo cikin rana ba takalmin

duk a dalilin sakacina

sannan nasa an dauko ki nasaki a gidan k'asa na dinga amfani dake sai da kika samu ciki yanzu gashi Abdallah ma na kasa bashi amsa balle Ahlan da Sahlan idan sukaji tarishin haifuwan su me zance musu ga Amira da Ameer da Abdulrahman suma bani na rad'a musu suna ba
bansan wane irin shukunci zan yankewa wanda suka cuceni ba
wai akan dukiyar abinda tun ina yaro nake kokuwan neman sa kota wane hali nayi shirka akan sa naso kusantan zinah a kansa Allah ya temakeni Ashe Matata ce
yanda naso dukiya ashe akan sa Allah zai jarabeni."

Ummuusulem tace "yawwa yanzu kashiga hanya Allah yace zamu iya jarraban ku ta inda mukeso dan mu kwada imanin ku kowa da tasa k'addaran ka godewa Allah daya tsaya a haka kaci gaba da neman kafara akan shirkan da kayi kaga de bokan naka dashi aka hada baki aka cuceka kuma ba malama ba kowaye yaje yace amasa aiki a kan ka inde yabashi ishehen kudi zaiyi kuma bai isa ya juya alk'alamin ubangiji ba yanzu abin yarage maka shine kanemi yafiyar Ruwaida dan tasha wahala tana da ikon jefar da Abdallah amma gashi ta kula dashi yazama mutum."

Mukaddam yace "ni ba Ruwaida bace ayanzu a gabana yaran nan k'anana su nafi ji
Ruwaida fa kunsan abinda tamin idan ita me kishin ubatane baza tamin abinda tamin ba Kharajina kirufe idon ki sosai dan zan hukunta Ruwaida duk da tana da aure."

Kharajina tace "amma ai ranta ne ya b'aci ko."

Yace "ai tasan bana cikin haiyacina kuma koda ina cikin haiyacina bai kamata tamin abinda tamin ba."

ganin ya dauki zafi sai fada yake yasa Ummusulem ta dauki yara tace mutafi aka bar daga Mudda sai Umma da jaririnta

washe gari abin yazame musu biyu ga zuwa kaduna ga zuwa meduguri suturan Ayya

sai rabuwa sukayi daddy Idiris da matar sa Maman Farida da Sahal da Ahabubakar suka kama hanyan meduguri
Sauran mutane kuma suka kama hanyan kaduna da jagora Mukaddam

Nan danan suka sauka dayake a jirgine

Gidan me kwano

Malama duniya ta mata daidai da yaran ta datake mutuwan so Ahlan da Sahlan komai nata Yana tafiya mata yanda take so

tana sama taga shigowan motoci tare da security din Mukaddam
da sauri tasauko k'asa tana rike da yaranta

Amma sai taji shiru tasan wata kila ya tsaya a bangarin Hajja ne amma ai ta hanashi wannan tsarin dan tafi son yafara tsauka a part dinta tawuce ajin taje part din Hajja ta masa sannun dazuwa kamar da dan haka tasamu waje ta zauna jiran sa

bayan Mudda ya gama gayawa Hajja komai da kuma shedu har da video din da Aminu yayi

Hajja rungume Kharajina tayi tafara kuka

" Kharajina
baki mutu ba
Kharajina ina cewa kece masifa a gidan Ashe makiran tana karkashina ban sani ba Ashe Kharajina ke alkairice
Mukaddam daya na haifa na baki kinzo min da dan mutum har 10 wanda 7 daga ciki nakine 3 na kishiyar ki da akayi adalilin ki lalle Khadija kece alkairi a zuriar mu
Hajara daga yau kinbar gidan na muguwa me fuska 2

Mudda yace "nikuma Hajja idan tamar gidan ai taci bulus me zai dameta tunda idan dukiyane matar nan tayi nisa
ba zamu koreta ma zata zauna taga yaran Mudda har goma suna yawo acikin gidan sai tafi jin haushi ta haka zan samu na rama abin da tabin dan ajiye komai zanyi na bawa yarana da matana tattali da son da wani uba bai nunawa yaran saba."

Hajja yan uwan ta dana mahaifin Mukaddam takira tace suzo akwai family meeting duk ataru tace wanda yaji yaga yawa wanda bai jiba

a part din Hajjan yabar su shi kadai ya karaso part din Malama

da fara anta ta tareshi tana cewa
  "Alhaji baza kadena zuwan bazata ba ko."

Murmurshi yayi yace "awannan zuwan nazo miki da abubuwan mamaki da

bazatan bari nayi wanka nafito yana maganan yana shafa kan su Ahlan da yaji wani irin kaunan su yasake nunkuwa a zuciyar sa
ya wuce sama binsa malama tayi amma yanuna kamar bai san tana binsa ba har ya bude kofan yashiga kafin tashiga ya banko kofan da karfi sai da malama ta fadi yaji faduwan ta da salatin da tayi amma sai ya nuna kamar bai sani ba

cikin takun isa yake saukowa yasha babban riga na shadda kyan sa da kwarjinin sa abaiyane yake hutu dajin dadi shiyake k'ara fito da kuruciyar Mukaddam ake kiransa da *Yaro da kudi* akalla yakai matakin shekaru 57 ayanzu amma baza kace yayi 40 ba shiyasa ake kiran sa Yaro da Kudi abokin manya
waya yakeyi har yakarasa sauk'owa

zama yayi kusa da malama

da tadafe goshinta daya kumbura

"lafiya malama na gankin haka meya samu goshinki haka."

"Alhaji wai zan bika na hada maka ruwan wanka ne baka san ina bayan ka ba katuro kofan amma na shafa magani."

"sorry maman 2 ina cikin farin ciki ne ina 2 sukayi.?

"naga alama tun shigowan ka kana cikin fara a
yau kuma a part din Hajja ka sauka."

"Eh hakan lefine."

"ah ah wai danan yakamata kafara shigowa kayi wanka ka shirya kadan samu nusuwa zata fijin dadin ganinka anawa ganin."

"yace hakane amma koda ganina ai kinsan banida wani matsala ina samun duk kulawa fiye danan wajenki kar ki damu."

kafin malama tayi magana Hajja da jama an ta suka shigo

cikin habaici take cewa
"masu gida sun zo me waje yazo yara kushigo gidan kune nan gida ga magadan gida tana rike da hannun Ameera da Hajara

Malama ta meke tana washe baki

tace" Hajja bak'i mukayi ne haka.?

"mutan gidan na gaskiya ne sukazo ba bak'i."

"to maraba da mutan gida."
Tace cikin fara a
amma idon ta yana kan Abdallah da yake mata mugun kama da mukaddam
amma azaton ta d'an dangine dan ga yan uwan sunan tare sake

zama kowa yayi amma ummusulem kusa da Mudda taje ta zauna daf kamar, zata shige jikin sa

Mukaddam ne yayi gyaran murya yace "Hajiya Hajara
wannan dakike gani itace Ummusulem tana da yara Ukku Hajara Nadrak sai Zaharin kingan su yanuna mata yaran
Matata ta ukku kenan

sai mata ta biyu
 wanda kinsan ta kece dalilin auranta yaranta 7
da karfi yace Kharajina tana inane sai asannan Kharajina ta shigo tasake wanka tasha kyu musamman zanen da aka mata a hannu na fulawa yasake fitowa da hasken fantan ta tasha nad'in cikin bakin liffaya tafara takun isassun mata har inda Mudda yake tasamu gefe ta zauna

afirgice malama ta meke cikin in ina take nuna Kharajina tace "Khadija yaushe kika warke?."

Mukaddam yace "tun sanda ta Haifi Ahlan da Sahlan tawarke."

"cikin tsoro malama tace Ahalan da Sahlan kuma?

Hajja tace "Eh mek'amata yaranta."

Malama tasake cewa "wai wanne Ahlan din wadannan na wajena garin yaya."

 Ita ma Kharajina
Cikin murmurshi
 tace "idan tantama kike ki tambarar idan neman sani kike kiyi *tambaya* nice Khadija Mustapha
maman Ruwaida da Abdallah da k'annen su ga sunan".

 cikin borin kunya Malama tace "mude tamu Kharajina ta mutu sai de me kamar ta ko kuma wani makircin a kaso a kullamana saboda neman duniya."

Ummi Mall tace "Eh hakan ma zai iya faruwa saboda yanzu duniya ake nema ta kowane hanya."

Hajja tace "Hajara alamun rashin gaskiya ya baiyana a gareki bake ki kayin tambayan yaushe ta warke ba yanzu shigowan ta kuka kika zo kina cewa ta mutu
Khajinan biyu ce da wada ta mutu da wanda ta warke
Tode kin haukata Kharajina kuma mijinta yasameta da temakon Aminu wanda shine yakaita dama daga nan Hajja takwashe komai ta gayawa malama

wani irin kuka Malama tasa ta zube a k'asa

Adaidai sanda yaran Mall suka shigo da boka auta
bayan sun masa laga laga da duka sun k'ona gidan sa da bukkan sa na tsafi

shima zubewa yayi yana kuka dan tunda yafara bokacci wani babban aljanin sa yace wanda Zai karya masa alk'adarin sa yarone matashi fari idan ya baiyana su zasu gujeshi dan yafi karfin su

Mall sojojin da yaturawa Auta dukka arna ne dan yasan basu da tsoro

yakalli dayan yace " Gud johny shine Autan ko."?

"yes Sir ."

Mall yace kaine auta me aljanu ko to ina aljanun suke har aka 'daukoka nan."

"Wllh tunjiya suka gujeni sukace lokaci yayi na tashinsu yanzu bana tare dasu yanzu ina nan amutum dina sai de ina neman alfarma da kasheni kafin na fara girban abinda na shuka na zalinci mutane na raba aure nakashe rayuka da bansan adadin suba."

Mall yace "ok shikenan tambayar da zan maka kafin na turaka gidan wahala daga cikin wahalan ka akwai yankan naman jikin ka abaka kaci shine abincinka har ka mutu."

"wani ihu yasa yace Mukaddam ka temakeni Wllh wannan shine wanda akace zaiga karshena dalilin sa yasa aljanuna suka gudu."

Mudda yace "Auta ni ba abinda zance a gareka sai nagode dan nima ta kaina zanyi wajen Allah nanemi tuban sa Kai ma kaje kayi dan haka ni yau ina cikin farin ciki
bazan hana Ismail hukunta kaba akan abinda kayiwa uwar sa."

Wani irin gurnani auta yafara yana dukan jikin sa kaman ninsa ne yafara canzawa
Mall yasa aka fita dashi

Hajja tace
"Hajara kifadi hukuncin da yakamata ayanke miki da kanki."

"cikin kuka tace "duk hukuncin da aka yanke min daidaine dan dukka alamomin munafuka ya baiyana a gareni

An yarda dani nayi zalinci anbani amana naci

bakomai bane ya jawomin hakan sai son zociya

wanda nasan dama irin wannan ranan zai sameni wllh Wllh na tuba tuntuni dan ko auta najima bana zuwa wajensa

Mukaddam kayafe min."

"yace nayafe miki saboda ina son nima Allah ya yafenin lefina wanda irin naki ne amma kisani bazan k'ara yarda dake ba."

tace "Mudda nagode da yafe min da kayi amma ina son ka yarda dani saboda nasan Kai mada ka tuba kana neman Allah ya yarda dakai duk da Kai zunubin ka baikai nawa da nasani Na take ba."

Mudda yace "wannan sanin ki amma bazan kyale abokan yinki ba."

ya kalli Kamal
yace
Kamal tun kana yaro katashi a gidan nan kasamu limi da duk abin bukata na rayuwa amma kacutar dani bayan nayar da dakai ayanzu zaka bar gidan nan idan ka kara koda Kallon kofan get dina asan nan zaka fuskanci hukunci

Sai ke yanuna Tabawa da take ta faman naso ita kadai tayi jakaf sai wani mannuwa take jikin kujera

Yace "kema bani da zabin da yawuce nace kibar min gidana dan bawani fansan da zan dauka akan ku na sadaukar dashi ga rayuwan yarana musamman Ruwaida da take wani hali Allah ya albarkaci zuri ana dalilin wannan cutan da kuka musu

Sai kai doctor Habib katuna kana almajiri na daukeka na kaika k'asan Germany kayi karatu duk da Hajara tasa ka amma dukiyata ce amma nima kaci amana na balle wasu

Dan haka baka can canci zama likita ba me kula da lafiyan dan adam zaka samu an rufe hospital din ka kuma kayi hakuri nasa an lalata takardunka tun ajiyan gudun kar kaje wani wajen ka cutar da sauran al umma."

Kamal da Habib kuka suka fara amma Mudda ya daga musu hannu

Suma Mall yasa aka fita dasu

Malama rarrafawa tayi ta kama kafan Hajja tace Dan Allah Hajja kuyafe min banida Kalma da zan kalli idon Khadija ayanzu na nemi yafiyar ta dan almarman Muhammad rasulillashi Hajja ki wuce min gaba."

Hajja tace "malama ko nace Hajara bazan taba yarda ki zauna acikin matan Mudda da yaran sa ki cucemu ba
amma tunda yace shi bazai sakeki ba yanema miki waje."

Da ky'ar su Baba Haruna suka bada hakuri abinka da manya aka sa santa Amma da sharadin.....

Borno

Anwanki Mama an shiryata aka koma kan Ayya matar da take wankan cikin mamaki take k'ara Shafa tuyan Ayya tace ikon Allah nikam Fanta taba jijiyar wuyan yarinyar nan kamar Yana dan har bawa nakeji."

wanda aka kira da Fanta tace" Aisa nima abin yabani makaki tunda nake taba gawa bantaba jin jikin gawa me zafi irin wannan ba kiji kamar me zazzabi bayan gawa sanyi gareshi."

"ai take matan suka fara cewa Anya tarasu kuwa kowa ya taba sai yace shima yaji jijiya yana harbawa zance har yaje wajen maza

Grema yanaji ya sunkuceta sai asbiti

Tunda Ayya da Mama suka kwanta jinya Grema yake da ayar tambaya akan jinyar su dayake lawyer ne yafara zarjin mutuwan da iftilain da yafada family daya acinkin wata 2 kacal

amma dayake hankalin sa ba akwance yake ba yabar case din da kula a

abubuwan a hannun Hassan babban a minin sa security s s ne

Hassan yana gudanar da binciken sa yafi bibiyar kanin Mama Bura dan yafi zargin sa haka asanda aka zo aka ce ana zaton Ayya da sauran nunfashinta yayi mugun firgita dan haka Hassan yasake sa ido akan sa

Ana tafiya da Ayya Bura ya tashi yashiga motan sada yake can bayan wasu motoci yajima sannan yafito yazauna acikin jama an duk da alamun bacin rai attare dashi
So biyu yana tashi yashiga motan yafito
.dan haka Hassan yatashi yazaga ta baya ya lallaba yashiga cikin motan da Bura yake shiga dan yana sa rai ko zai kara shigowa

Baya ya shiga kasan kujeru ya kwanta ya setting camera sa yayi lub ya kwata yana Allah Allah yakara shugowa
aiko bai jima da kwankiya ba yasake jin anbude anshigo

Buran ne

magana yafara a wayan sa a handsfree wayan take dan haka Hassan yanajin duk amsan da wancen yake badawa

haba doctor ya zaka bata min aiki Wllh inaga da gaskene bata mutu ba baka san nafi son mutuwar yarinyar fiye dana uwar ba."

Daga jan doc yace "Sir nasa Alluran ne a gaggauce kasan sai da na kashe na'uran d'akin kuma idan na'uran yayi
1minute a kashe za iya gano ni shine ban sa aluran duka cikin Drip din ba kuma ruwan bai shiga jikin ta sosai bane dan ban samu time din da zan k'ara gudun ruwan ba shiyasa ina ganin dogon suma tayi
amma kaga drip na uwar dayake na k'ara gudun ruwan ita yashiga jikinta
Amma sir Kai ka bata min aiki ai sai da nace kabari a yiwa mutum daya daka baya sai ayiwa dayan kace kaide sai dukan su 2 sun mutu atake

Kaga ko dole asamu matsala kayi addua ma kar asirin mu yatonu dan idan an mai data india asirin ne zai tonu dan za ayi kwaji sosai akan abinda yasata dogon suma har na kwana 2

"doctor me mafita."

"ai ni bani da wani mafita Kai ka bata abin taya zaka ce mutum biyu makusan tan juna sun mutu rana daya lokaci daya a hospital daya wani zargi bai biyo baya ba
Hakan ma wai ni nayi gaggawan sallaman ku dan kar ayi bincike akan gawan

kuma Wllh idan aka kawota nan zaka min sana din aiki da hukuncin kisa dan nan ba Nigeria bane."

"zansan yanda zanyi ba za akawota nan ba."

Doctor yace"OK Sir nasan tunda aluran nan ya taba jikin dayuwa ta iya rayuwa sai de idan tana da rabo me yawa zata mutu ma."

"OK doc zan sake kiran ka duk abinda ake ciki'

Da harshe turanci suke maganan

ya kashe wayan ya sake fita

Jinjina kai Hassan yayi yace ko ahaka aka tsaya ansamu sheda

Ahankali ya zame yafito yakira yan sanda suka zo suka tafi da Bura da sai hauka yake yana
cewa "menayi to koma me nayi ai zaku bari ayi suturan yar uwata dani haka suka hankada k'yar sa

suka ce idan munje kaji

da ky'ar likitoci suka samu suka gano Ayya tana da sauran numfashi amma tana cikin mawuyacen hali ansa mata alluran guba ne

Sahal yace Girema tunda akwai jet a hannu nake ga su bamu doctor cin da zasu na kula da ita ahanya mukaita Germany wajen kanina Khalifa abin da yakaranta kenan fitar da guba dan ya kware wajen aikin sa shiyasa ma turawan suka rikeshi."

Grema yace "nagode abokina."

Hassan yakira Grema yagata masa yanda abin ya kasan ce

yace "to a kula dashi mu yanzu zamu wuce da Ayya amma kada ayi suturan ita mamar ma akawo asake kwada ta."

atake aka wuce da Ayya

Ita muka mama an tabbatar da tamutu akayi suturan ta

Affan yace "my love mu koma ko kinga Daddy Idiris fada yakeyi meyasa kika

zo."

Ruwaida da muryar ya dashe dan kuka ba ataba jin abinda take fada
ta jawo pepper
tayi rubutu akai kamar haka

my dear nagode da kulawan ka dan Allah ka koma wajen aikin ka kar karasa aikin ka zamu koma nida Kharajina yazanyi Ayya na rasata na hakura

Yace "Eh my love zan dawo ina kaiku dan nafi son na dank'a ki hannu doctor din da nayarda dashi kinga abinda yafaru da Ayya Ina tsoron duniyar nan my love kar acutar min ke

Murmurshi tayi ta rubuta
ku dena yaudaran mu akan cewa Anty Ayya bata mutu ba saboda mun damu wato mudena damuwa ko acikin tafin hannu na numfashin ta ya dauke

"Wllh bata mutu ba yanzu haka ankaita Germany wajen yayan ku doctor

Ruwaida wani murmurshi me ciwo tayi dan tasan mutuwa 1 ce

Bura ya doku iya dokuwa cikin wani waje aka sashi ana gana masa Azaba akan yafadi gaskiya

Zan fada
Ni sunana Ibrashim ni kani ne awajen Kangiram ina jin haushin yanda ta fifita mijinta ta dank'a masa uban dukiya

Shine nayiwa yaran su asiri suka lalace Amina da Muhammad suka auri juna ita kuma Bilkisu nasa mata hauka amma da yake tana shaye shaye sai akace shi ya haukatata dama shaye shayen mani ne sila

AMINA da modu nabisu har kasan da suke da sunan nine kad'ai me sonsu na kawo musu ziyara

Sai da nabari yasha giya yakoshi nace yaje airport ya dauki jirgi suyi yawo da yake dama drivern jigine
Shine nace harda yaran da AMINA shine suka tafi ya dauki jirgi wanda yake dama mallakin shi modun ne

Yana shigowa na fara masa kirari
yayi d'ana yau fa asaman ka kake."

Dariya yayi yace "Baba Bura baka yawa fa."

"Eh mana yau yanda kage hakan nan kyanta ka hau gajimaren gasken yaka mata kahau hugaban matuk'a na duniya."

Yace "Baba Bura bar hawa saman nan banida passenger
kasan ba kowane k'asa nake zuwa ba saboda tsaro."

"haba Modu na kuma dan baka da passenger
ka kasa daukan family ka ku shakata kaida jirgin ka."

"kakawo shawara fa Baba Bura ba uban da ya isa ya hanani jirginane kudin ubana nasato na tsiya yau zamu kwana muna shan iskan sama."

daga nan ya dauki Amina da yaran su biyu suka fita

yana tada jirgin basu wani jima ba yakife shikenan nagama dasu

Sai shima Duno ni nasa aka masa alluran mutuwa asanda ake shirin fita dashi

Sai ita Ayya akan idona suka je asbiti bayan fitan su naje wajen doc da niyar nace yasa mata jinin me HIV dan Greema yafara auren ta bayan natsiyi doc yake gayamin ai jinyar da yake jikin Ayya yafi me HIV hatsari amma bayi karfi ba zata iya warkewa ko akasan nan ma
ciwon hanta ne."

nacewa doctor idan akwai alluran da zai karawa Ciwon karfi dan Allah idan sun sake zuwa ya musu Na fadi kudin da zan biyashi

dariya yayi yace to ai ni ko results din ban masu ba dan bai fito ba nace sai anjima idan suka zo sai na mata akwai alluran da zai k'ara karfin ciwon zanne ma yanzu

Haka ita ma yaya Kangiram aka sa mata wanda zai karawa ciwon ta karfi har mukaje Indian din na siyi wani babba likita yamin aiki akansu

Ina murnan saura Barrat da Bikisu a hankali suma zasu bisu

Banyi dan komai ba sai dan nasan idan babu wadan nan mutanen nine magajin dukiyan su.....

Tofa duniya juyi juyi ashe akwai wanda yafi Duno taddanci kenan

Menene sharadin da Mukaddam yace zai gindayawa malama da kukuncin da yace zai yan kewa Ruwaida

Awannan fansan duk na malama yafi sauki ina son tuna tar daku cewa bakin mutane Yana tasiri acikin rayuwan dan Adam gashi de duk tsiyan malama komai yana shirin zuwa mata da sauki badan komai ba sai dan bakin al umma da suke mata addua gamawa lafiya dan mutum ko mutuwa yayi Mala iku suna rufe file din sane da abin da mutane zasu ce a kansa Allah ka kai masoyan mu kan gawan mu idan tamu tazo

Ameen

*B Jattko**AMFANIN SOYAYYA*
aure

NA

BATUL ADAM JATTKO
Ashbat

kainuwa asso

20

A
Germany
anyi aikin Ayya cikin nasara har tafara magana Hamrah da wata kanwar Greman ne suke zaman jinyar

Anyankewa Bura hukuncin kisa

Anyi bikin Wassilim Kabir sankira da Ammati Nabil shiddams

Da Juwairiya Kabir Sankara
da Akram Nabil Shiddams

Anyi biki irin na kece renin nan
Amma ameduguri
Dan daga gidan su Hamrah komai a sanyaye akayi dan Hamrah ma batazo bikin ba dan tana wajen zaman jinyar Ayya

Ruwaida tasamu lafiya da tawarke a cancer din doctor da zai mata aiki a mahaifa yazo sai yaga mahaifan Ruwaida ras yawarke bawani aiki da za ayi mata dayake dama tsagewan bakin hamaifane ashe maganin da yabata tana sha yawarkar da wajen su Kharajina anyi murna sosai rungume Ruwaida tayi tana cewa "sis budurcinki yana nan

Gidan Mukaddam

Umma da Ummu suna yanda suke so malama takoma kamar bata gidan haka Abba yadauki kulawa na musamman yabawa matansa da yaransa sallah kawai yake tadasu shima jam I yake jansu

Malama ganin abin take har yanzu kamar a mafarki wai larabawa take kishi dasu ita kam ta sallamar musu sosai malama ta sake runguman Qur ani da dagewa akan daliban ta na islaminyan cikin gida idan abin yamata zafi zakiji tana karatunta tun karfi dan fitar da lafazin Qur ani yana yaye damuwa

Ahlan da Sahlan idan zasu shiga part din malama Ummulsulem hanasu take yauma kamar kullum suna zaune a dinning sai dariyan su da shewa kakeji malama da tun asuba take masallacin islamiyar ta dama na mata ne tazo wucewa ta murmurshi tayi ta karasa inda suke dafa dinning table din tayi tana kaida Mudda amsawa yayi kawai yaci kaba da abin da yakeyi
Yace "Allah my Kharaji sai kin karamin to ke duka ke zaki ci saboda baki taba zuwa gona kinga yanda ake noma ba ko yajawo filet din gamasa ita ma Umma tajawo kokuwa suka fara saida sukayi ta adi a dinning table din daga karshe de ita Umma ce ta kwace tayi nesa can parlour ta tsaya tana

cewa" ni zaka cewa ban taba zuwa gona ba nafika sanin meye gona kaida kayi rarafen parlour nida nayi acikin Sahara da gona

Taya abincin nan zaimin yawa ka manta cikin jegone."

Ire iren wasan ninan shikawai ake agidan

Sosai suke abinda suka ga dama dan ma metaya su Hajja ta tafi India duba Ruwaida

Malama da tagaji da tsayuwa ba wanda yace mata tazauna balle a mata tayin abinci ga lafiyayyun abinci irin na larabawa Ummusulem da kanta take shiga kitchen tayi

Malama Shafa kan Sahlan tayi tace "yarona ba gaisuwa ya school kwana biyu bakwa zuwa bada hadda fa."

Ahlan ne yace "Ummul ce take hanamu zuwa wajenki wai ke muguwace."

Malama ta goge hawayen da yazubo mata ta Kalli Abba tace "Mudda dan Allah ka gayawa matan ka zasu iyamin kowane irin horo amma dan girman Allah karsu horeni da rabani da Hassan da Hussaini."

tana gama fadan haka ta juya da sauri tabar wajen

Ummusulem taso mayar mata murtani amma ta kasa tarasa dalilin da yasa malama take da mugun kwarjini duk abinda tayi niyar yi mata idan tazo gaban malama sai ta kasa yimata koda kallon banza ne
Ita ma Umman Ruwaida haka Kai shima Mudda malama mugun kwarjini take masa

(Wannan sirrine na falalan karatun Qur ani da salatin Annabi)

India

Ruwaida manne da waya sai faman shagwaba take zubawa Affan

"haka fa kace zaka zo ba kazoba har an sallamemu yanzu muna gidan Abba na Banccop

ah ah basai gazoba nayafe dan gobe zamu tashi missing too much my dear OK".

ta kashe wayan tareta kissing din sa

Hajja tabe baki tayi tace inde wannan Mijin naki me kiran samudawa wanda ya gama da boka Auta ma balle ke zaki gane kuren ki idan kika hada daki dashi wannan Mijin naki da nagani Marar annurin fara a
ba sumbata ta waya ba zanso naga kina kissing din nan afili marar kunyar

karya."

"Dakata Hajja bangane me kiran samudawa ba kuma wane boka auta yagama dashi dan baki san waye Affan bane?."

" Ismail de niko na ganshi dan gidan Hajiya Ruwaiyatu soja."

murmurshi Ruwaida tayi tace" bakiji daidai Hajja."

"ke gidan ku ungo naki ni zaki cewa banji daidai ba anuna shi yana wani cinkunu ace shine Mijinki ki zauna kina cemin banji daidai ba karya na miki kenan."

"ah ah Hajja kinde fadi ba daidai ba."

Cikin mamaki Hajja ta cire wasa tace "yanzu dawa kike waya."

Ruwaida tace "saurayina ne Affan Suleiman"

Hajja waya ta dauka tana duba number har taje kan Umma tasa wayan hands-free
daga can Umma tayi sallama tana gaida Hajja

Hajja tace "lafiya Khadija wai ni ya sunan Mijin Rawa ma."

Hajja "Ismail sunan sa yanzu ma yaya tasa ranan tariyar Saturday de idan kunzo Wednesday saboda ansa ranan auran sada HALIMA yaya tace sai Ruwaida ta tare amma kar ki gayawa Ruwaida bata san zancen ba zuwan naku goben yana nan ko."?

"Eh."?
Kawai Hajja tace tare da kashe wayan dan ganin yanda Ruwaida ta wani firgita amma ko motsi ta kasa yi

"Hajja da gaske ne an auramin Yamall?
Wllh ba nason sa ni Affan nake so ya zanyi da soyayyar Affan yamall baya sona ya tsaneni."

"bangane ya tsane ki ba kuma waye Affan din Aisha ina raye ba aissa amiki abinda ranki bayaso ba kinsha wahala yanzu dadi zaki cigaba daji

Ruwaida ta kwashe duk abin da Mall ya mata tagayawa Hajja sannan ta gaya mata waye Affan

"barni dasu mukoma gidan tukun za a juya komai yanda kike so."

Nigeria

Hajja tace
"Mudda ya akayi kace awuce da Ruwaida da Kharajina Kano danme ba zasu zo gida ba."

Mudda yace" Hajja Ruwaida tamin lefi ina son zan nuna mata kurenta nace kar a hadaku mota daya kuma wanda ya dauki su Ruwaida ya wuce Kano da ita gidan me walwala
amma nima inason ganin ta sosai hakan bazai hana na hukunta taba."

Umman Ruwaida shiru tayi
Ummusul cema tace "to Abba haka zata tare baka sa mata albarka ba."

"nasa mata albarka Allah yasanya alkaire acikin rayuwanta."

dariya Hajja tayi tace "amma zasu sha drama dan nima da k'yar na lallaba Ruwaida na kawota wai ita sai an raba auren dama ina tunanin yanda zamu rabu lafiya shike nan ma nida tagan ni saita tare wata kila ma sai ta samu ciki Ruwaida rigima amma ko zata dangana da wannan Affan din sai anyi mata rubutun dangana."

Murmurshi Abba yayi yace "bawani rubutu zata hakura tasan cewa tayi dace da miji."

Hajja tace "shima ja irin kishi yasa yana wani cewa baya sonta dan kuruciya a yana yin labarin su nagane yaron yana mugun sonta wataran zasu zama abin alfahari Insha Allah."

Itama Umma murmurshi tayi tace "ai son da Ismail yakewa Ruwaida yayi yawa shiyasa ma banyi maganan araba auran ba wataran zasu jone azuba musu ido kawai nida yadin ga zubar da hawaye a gabana."

Kano

Kuka sosai Ruwaida take
"Ummi an cuceni an hanani Affan Ummi Allah yanzu ba ko digon son yamall azuciyata Affan nake so
Wllh Ummi idan Affan yarasani zai mutu nima bazan juri rashin saba
Kuji tausayin mommy sa shi kadai ta mallaka."

Mall da yake gefe murmurshi yayi azuciyar sa yace idan zama da aurenan shizai sa miki bakin ciki har mutuwar ki yarinya zaki mutu kowa ya huta
bari ma afara wasan tundaga yanzu

Afili yayi gyaran murya yace Ummi ki lallameta ki bita a hankali zata sauko nasan abin da namata ne yab'ata mata rai amma zata soni insha Allah."

cikin mamaki Ummi ta kalle shi
tace Ismail abinda kafada har cikin ranka ne kanason Ruwaida yanzu."

"Serious Ummi ai dama kawai bata min rai tayi yanzu na huce my Ruwa ki yafe min yayi maganan yana dago mata gira."

Ita ma Ruwaida da mamaki take kallon sa sam ba alaman gaskiya a tare dashi

Ummi tace to shikenan Ruwaida akwai lefen ki adaki kiduba abinda baiyi ba kuje kedashi kusake aunty ku Abida ceta hada
Sannan kije gidan hawa biyune ne kizabi wanda kike so ko hawan farko kona karshe gobe za amiki jere Baban ki yayi kokari da keda Hamrah yamuku kayan da nide duk yawo na ban taba ganin saba kinga kayan."

tana gama fadan haka Ummi ta meke tayi sama

tabarsu nide abin duniya ya isheni saide nama sawa raina Affan ne kawai mijina dan bani da wani tantama tunda ina da Hajja nasan zata juya komai

Maganan da naji yamall yanayi ne ya kase min tunanina

"kina tunanin yanda kikayi sa an samun tsadadden miji kamar ni ko?

Murmurshi yayi yace to baki samu ba gidana kamar mak'abarta yake a gare ki dan haka ina baki shawaran tarewa da nikkafanin ki
sannan naji Ummi tana cewa wai kije ki zabi part din da kike so to bari na gaya miki sama na biyu yamiki tsada dan da hannuna na bada kudin da aka ginashi da sunan *HALIMATUS SADIYA SASHIBA*
ina gargadin ki dacewa ki zabi na farko
Congratulations kinyi nasaran auren
Ismail Wakili walwala
ayanzu lokacine da zaki san shiwaye yana gama fadan haka yafice

tabe baki nayi nace ni AISHA nafi karfin ka sai Affan

waya nane yayi kara ina kanin me kiran nayi murmurshi nad'aga
kuka naji Mommyn Affan tanayi

"Ruwaida Affan ya karaso ko ya mutu a hanya Ruwaida Affan Affan Ruwaida."
"Subbahanallashi mommy me yasamu Affan din?

A gigice nake tambayar ta

"yanzu yashigo yake gayamin wai Ummin ku tagayawa Kharajina tabashi hakuri wai an daura auren ki da dan uwanki Ismail shine yana gama gayamin yafita da gudu kuma yaja motan da gudu shikenan zan rasa Affan."

Mommy insha Allah bazai mutu ba kuma auren kakata zata raba ta bani Affan."

tana gama Fadan haka ta kashe wayan ta fita da gudu adaidai sanda Affan yayi parking

Balle murfin moton yayi yafita agigice yana haki abinka da fari duk faskan nan yayi jajir dashi

Ruwaida murnan ganin yazo lafiya bata san sanda ta fada jikin saba shima runguman ta yayi

yace "dan my love kice Kharajina wasa take min."?

Murya sukaji abayan su yace "gidan walwala ba gidan karuwai bane ku nemi gidan karuwai muna da kanne kar ku bata musu tarbiya
Idan na kara ganin kafan ka agidan nan iyayen ka zasu gwashi kwakwalwan ka anan kuje can inda kuka saba had'uwa da."
Inji Mall cikin wani irin tsawa

Kafin Affan yace wani abu sukaji muryan Baba Haruna ma Yana cewa subbahanallashi ya haka Aisha ya haka ina ganin ki kamar me hankali kike wasa da aure haka ai ko ba aure abin da kukayi ya haramta a addinin mu."

Mall ma yakara da cewa Baba kuma agaban din bin jama a nan na haraban gidan nan sukayi haka inaga idan suka kebe haka fa yayi zaman jinyar ta a India wllh ni dan haushi sai barmusu wajen nayi nazo."

Ruwaida sai alokacin bugun zuciyarta yadan lafa ta janye jikinta daga na Affan tazube kasa shakaf da wani irin kunya

shiko Affan kamar andasashi Kalman Baba ne kawai yake dawo masa

Aisha ya haka inaga kamar kina da hankali da aurenki kike wasa da aure haka...
wannan Kalman ne kawai yake dukan dodon kunnensa masa

Ahankali yafarajin zai iya d'aga kafan sa yataka har gaban Baba Haruna
hannun Baba yakama cikin wani irin murya yace "Baba da gaskene dama anyiwa Ruwaida aure Wllh nafi major Ismail son Ruwaida zuciyata bazata ina juran rashin taba."

Yana maganan yana dafe kirjin sa ."
Adaidai lokacin mommyn sata karaso

Baba Haruna dama yasan HAJIYA HADIZA shugaban alk'alai dan haka kama Affan yayi yace mushiga ciki ayi maganan
Family meeting a ka kira kowa ransa ya baci akan abinda Ruwaida tayi amma kowa yaji tausayin Affan da mommyn sa dan sai kuka suke mommy tana neman alfarman dan Allah a warware auren abawa danta

Shiko Mall har yafara murna zai rabu da Ruwaida cikin sauki ba tare data tare masa gida ba

Ummi tace "hakan ne HAJIYA bazai samu bashi Affan ba musulmi bane bai san kaddara ba koke amatsayin kina shugaban alkalai hakan yayi daidai ne tsaban son d'a da son zuciya yayiwa mutane yawa kota wacce hanya sai anbasu abinda suke so kenan ko.....

Mommy tace
"Dakata nan ba kotu bane shiyasa ma nazube a gaban ku nake kuka dan inda kotu ne saide kuzube min dan haka kubar maganan wani shugaban cina Affan daya na Haifa kuma shi nasani akan sa zan iyayin komai Ruwaida yake so kuma zai samu."

Hannun Affan taja yatashi su fita yaki yaci gaba da kukan sa Yana cewa "mommy dan Allah ki bisu da lallami ni abani my love na."

Sun kuyawa tayi ta rada masa wani magana a kunne da karfin yameke yana murmurshi zasu fita ita ma Ruwaida tace "dan mommy kiyi wani abu kar narasa Affan."

Murmurshi ta mata tace "hadin kanki nake nema Ruwaida inde nasamu komai zai iya yuwuwa."

Tana fadan haka tajuya su kafita

kowa Sai da ransa ya baci da abinda Ruwaida tayi Ummi harda marinta daga nan kowa yaci gaba da yimata nasiha akan aure da kaddara duk da tuni ne akan abinda tasani amma sosai jikin ta yayi sanyi

Suna zuwa part din Ummi
Ummi tace Farida raka ta tazabi part din daza a mata jeren anfasa sai asabar din a goben zata tare a huta kuma bani wayan ki."

Ruwaida ta mek'a mata wayan tana kuka

Ummi tace "kuma a cinku duk wanda ya dauki waya yabawa Ruwaida dan tayi waya Wllh ni da itane tanuna Nafi da Farida da Kharajina

Part din Mall
Wow suka ce suna shiga kasan duk parlour ne wamda girman sa ba amagana sai babban kitchen
tun kafin su hau suke cewa hawa nabiyu yafi na daya kyu duk da fentin iri dayane amma tsarin da bambaci

saida suka duba hawa na dayan shima yayi ba lefi d'akuna 5 ne aciki sai kitchen da parlour 2 iri daya dana Sahal

Suka hau na biyun ai bude baki sukayi yayi mugun haduwa har yafi part din iyayen su kyu gashi ba wabi tarkacen d'akuna daki 2 kacal sai kitchen duk parlour yacinye saboda girman sa dan falo ne iya ganin ka haka dakunan ma manya ne

"Kai ga kicin sai kace a turai har yafi kitchen din aunty abeed kyu ai nan zaki zafa sis."
inji Nafi
murmurshi Ruwa tayi da tatuno warning din Mall amma dayake itama kwanan kantace tace" Eh ."

Ayya tawarke ras sun dawo Hamrah ta koma adamawa dan shirye biki

Mall yayi mugun jin haushin yanda Ruwaida ta zabi part din su bayan HALIMA ya ginawa amma idan yatuna tarkon da ya dana mata sai yayi murmurshi

wai wacece HALIMA

Halima Musa y'ar gidan wani drive ne Musa wanda a gidan su Ruwaida da Ayya yake aiki na hutoro

Ayya ce tayi ta damun Ruwaida akan taje duba su Cabaliya dama ita suka barwa digan Ruwaida ita kadai ta tafi dan su Nafi suna makaranta

Tanayin horn megadi ya lek'o jiki na rawa dayaga Ruwaida dan mugun tsoronta sukeji

Shijaf har kasa tafito ta rufe kofan motan tana sanye da farin glass tayi kyu dan Ruwaida komai tayi kyu yake mata
Ita tafara gaida megadin da sauran Ma aikatan mutane 3 awajen harda Musa baban Halima

"Baba garba ina kwana ku."

Abin yabawa ma aikatan gidan mamaki
Ka rasowa tayi inda suke

Tasake cewa "Aunty Ayya tace a tambaye ku kowa yaga alert ko."?

Musa yace "Eh Hajiya mun gani har da Karin kudi aka mana wannan watan."

Murmurshi tayi tace "to kuyi Addua Allah yakara daukaka Aunty Ayya yakare tada shirrin makiyan ta."

Malam Tanimu me wanki yace " wannan kudi da ake ta bamu bama aikin komai anya halak din mu muke ci kuwa.?

Ruwaida tace
"Ai ita ta baku halak din kune
kuma ba kuna yiwa cabaliya aiki ba."?

"wallashi ranki yadade bawani aiki agidan nan yanzu"
inji Musa

Murmurshi tayi tace to shikenan Baba MUSA dama Aunty Ayya tace zata yi sharawa daku idan kun yarda zakuyi aiki a meduguri zata baku aiki a companyn ta amma sati me zuwa zata zo sai tazabi wanda zata dauka."

Godiya suka mata tashige ciki

Cabaliya tana ganin ta tace "wanake gani kamar uwar dakina Ruwaidatu."

bayan sun gaisa Cabali tace "ai bansan kinzo ba yajiki."

"da sauki nazo shikaran jiya gobe ne ma zan tare."

"wai ni uwar dakina acikin yaran walwala waye babban soja zaiyi aure kwanan nanne?

Rawa tace "Ismail ne."

Cabal tace "ai yar gidan Musa direban kune Halima
Shiko yaron me yake gani zai daukawa kansa jaraba ai sai da naje har gidan dan nabawa iyayen naku labari wacece HALIMA folisawan get din suka hanani shiga nayi nayi sun hana ai sam Halima bata dace da irin wannan gidan ba."

Ruwaida tace "to ai gwara da suka hana ki irin kune masu kai suka a bata sunnah ko?

"ba haka bane uwar dakina kinsan de bazan yiwa Musa bakin ciki ba kituna dan dakinane ni nakawo muku shi gidan nan ma amma hakan bazai bari na bari acutar da gidan kuba dan kunmin rana

Halima auren ta 3 duk ka mazan suna rabuwa da itane akan halinta na bin maza da mata ita

Daga nan tafara bata labari

Halima itace babba a yaran Musa tun tana budurwa tayi ciki aka zubar mata sannan akayi auren ta anyi aurenta da wata 5 ta haifu mijin yace ba nasa bane tazo gida tareni danta Sadik
 Tasake aure Mijin ya kamata da wani yaro me shiga gidan dama ya kamata da wata k'awar ta suna madigo amma aka basa hakuri ya hakura sai da ya kama ta da namiji yasaketa tafito da yaro daya a nan ma

Duk cikin goron dutse waye baisan Halee kyan bariki a gani a gida ba

Yanzu haka bata jima da yaye yarda da ta haifa shegiya ba

Samari da matasa

Idan sun ganta kirari suke mata suce Halee kyan bariki

sai tace a gansu a gida suna yawo

Kin san ma anan a gani a gidan da take cewa."

Ruwaida ta girgiza kai

Cabal tace "to aga yaran shegu suke nufi idan suka ce kyun bariki sai tace a gani a gida

Yaranta 4 daya ne kawai dan sunnah

Danaji wannan sai da naje har gidan dan na tambaye ta wai garin yaya tasamu wannan Mijin me tsada
Kinsan gidan Musa ba bakona bane ko matan sa sunyi fada ni yake kaiwa namusu sa Santo sannan ina musu alheri sosai nasan kinsan tsakanin mu

Goron dutse
Gidan Musa
Halima murmurshi tayi tace "Mama Cabal zaki ce tayaya nasa meshi Allah yabani shi wata rana rashin kudi ya matsoni kona abinci banida shi kawai gidan yayar mamar mu ya fadomin a rai tunda gidan masu kudine nayi wanka nasa dogon shijaf dan nasan mijin ta malamine idan naje da shiga irin wanda nada nakeyi a nan ba barina zatayi ba

naje tsallaka titin yankaba zan shiga cikin sauna dan tunda ga bakin asbiti a daidai yace kudina ya kare a kafa natako na gaji ban kula da hanya ba na wuce kawai sai jinayi mota ya turani gefe Allah yasa bai takani ba yayi parking ya fito wani farin saurayi kamar balarabe yake ta bani hakuri yace nazo ya kaini asbiti

nace "ah ah Wllh banji ciwo ba wannan dan gurjewan ma faduwan da nayi ne zan iya tafiya."

"ok amma dakin bari na Kai ki ".

"ah ah bakomai"
 nace dashi

"OK kibani numbar Mijin ki ko wani matsalan zai biyo baya nima ganawa yabude motan sa yabani katin sa."

nace "aini banida waya agidan mu ba a barin budurwa ta rike waya amma me yasa kamin kallon me miji."?

dago kansa yayi yafara kallona
Yace da gaske kike ke budurwa ce yanayin shigan kine yasa na zaci matar aure ce ke."

Murmurshi nayi nace "ai haka yan GIda mu suke

"To zan iya sauke ki a gidan ku dan naga gidan dan Wllh najima ina neman irinki."

"Gidan yana nan sauna idan kace gidan malam Zakar me azama kowa yasani."

"to shikenan amma wannan kam baki isa kice bazaki Karba ba".

yame kamin rafan dubu dubu guda 3 dubu dari ukku

naso namusa saboda na tabbatar masa ni salahace amma yamasa na karba mukayi sallama

Ina zuwa gidan aunty Kubra nazube a cinyar ta na tsara mata komai da bukatata na zama a gidan ta har nasamu na auri Ismail dan nasan idan a goron dutse ne bazai yuwu ba

Ta amince saboda tana son na shiryu Mijin tama ya abince zai zauna a matsayin Babana kinga tsakanin sauna da goron dutse ba mezuwa yamin muna furci yanzu haka nazo gidan uwar dakina Sa a zata rakani asbiti a min d'inki nakoma budurwa dan ba maganin da zan sha ya mayarni muburwa a yanda nake a fafaren nan sai de a dinkani."

"To kinji wacece HALIMA zaki so ta shiga Zurian ku."

Ruwaida ta numfasa tace kishiyata yar gidan driver na

Afili kuma tace Cabal Dan Allah kar ki hana auren nan kibari tayi wata kila tsilar shiryuwan tane kiduba kemafa kinyi bariki muma munyi ina tausayawa duk matar da take bariki kinga Halima mijina zata aura amma bazan iya sawa a fasa auren ta ba duk tsananin son da nakewa yamall kullum sai yamin abinda yaka mata ace na tsane shi amma sai naji son sa yana kara nunkuwa acikin zuciyata amma nafi karfin zuciyata bana nunawa kowa haryanzu ina son sa banda Ayya da Hamrah ba wanda yasan nayi murnan auren nan duk da ina son nemawa Affan mafita

Dan Allah karki tona asirin Halima kibari yacika gidan sada yan barikin."

"Shikenan uwar dakina yanzu gobe ne tariyan kibani number da zan sameki kinsan wadan nan folisawan naku sai anyi kira an tabbatar zasu bari a shiga."

Ruwaida tace "yi zamanki Cabal ban gaiyaceki ba da yawan magananki nan ai gobe kikace je gidan sai kowa yasan wacece HALIMA."

har wajen mota Cabaliya ta raka ta sai data fita takoma ciki
Ruwaida ta danyi nisa da gidan motan ta yatsaya cak
Tana dubawa taga danjan mai ne yakama dukan sitiyari tayi dan bata san ya zatayi ba gaba waya a hannun ta Ummi ta kwace
gashi duk titin anguwan ansanta shiyasa ta fito da mota me bakin glees
Aiko tana fitowa samarin anguwa suka dau ihu
KALA KALA ABASU KALA ABASU KALA RUWA RUWA

Duk idan sunzo wucewa sai sun mata wannan kirarin danma fuskan a murtuke yake batsa tsayawa

Wani tasamu da tasanshi ta aikashi yasiyo mata mai

tana tsaye wani mota yawuce ta motan tabi da kallin dan kamar tasan motan

Mall ne da abokin sa Mujashid acikin motan "Mujashi yace "dakata Mall wata nagani kamar Sis dinka Kharajina."

Mall da yaga Ruwaida sarai
murmurshi yayi yace "baka kalleta daidai."

Mujashid dama shine yake jan motan baya yayi dai dai sanda wasu samari suka zo wucewa suna kara yiwa Ruwaida kirari

Mall yace Kai kaji kirarin tama ina ga wannan wata me siyar da hajace fa kai ko dama dan hannune kasamu".

Mujashid yayi murmurshi yace" Wllh kuwa naga alama amma wannan macce .me tsada haka gakuma shigan mutumci."

"bakaji kirarin da yara suke mata ba kai de ka taya kozaka dace."

Mujashid yace "haka za ayi dan Wllh na kyasa."

Yabude kofan yafita

Sai da yabari ya karasa inda Ruwaida take
Dakarfi Mall yadaga murya yanda Ruwaida zataji

yace kafin kayi amfani da ita kaje a Amata Tast na HIV dan Wllh idan ka kaso bazan baka kanwata Nafisa ba."

Aiko taji dan saida suka hada ido da Ruwaida

Mujashid
Ya karasa inda take

Shikuma Mall yafito yazaga yashiga bazaunin direba yaja motan da karfi

Ruwaida ta Kalli Mujashid tace ba damuwa na amince inde Mall yaturoka wajenan

Har dare Mall shiru baiga zuwan Ruwaida ba kuma gashi abokin sa idan yakira baya dauka

Daurewa yayi yace Ummi wai ina Ruwaida tajene."

Ummi tace "Wllh fadan da mukeyi da Abida kenan tun dazu tafita wai zataje duba ma aikatan wancen gidan nasu nace ta dawo dawuri za amata kunshi amma shiru ba labarin ta gashi ba waya a hannun ta kuma agidan nan ba wanda yasan gidan Sai Sahal shikuma yana adamawa yanzu na tura masa Test yaturo min address din gidan baiyi Ripley ba ina gama bai duba ba kasan halin Sahal
Me kunshin har tagaji duk anyiwa kowa ita ake jira ni tsorona ma kar ta gudu dan bason auren take ba Wllh ina gudun aikin danasani.....

Mall bai karasa jin maganan Ummi ba yafito yana cikaba da kiran Mujashid

sai asannan mujashid ya dauka cikin fara a yace Mall kana damuna fa kana rage minjin dadi....

cikin wani irin murya Mall yace "Mujad kana nufin wanan karuwa ta yarda dakai kuna tare kenan."?

Mujashid Yace "sosai amma kadena kiranta karuwa sunan ta Ruwaida kaga banzo ba ko yarinyar ce mezafi ce ta hadu karshe Ashe a Africa ana samun irin su."

"da gaske kake ta amince da kai.?

Mujad yace "sosai gamu ma a w w Hotel amma yanz.....

Awani irin tsawace Mall yace whattt!!!!!!? tare da jefar da wayan yazari key din motan sa kamar zai taka megadi yayi han yan hotel din daddy sa W2

Tofa banji comment dinku sosai ba a pg 19 shiyasa ban kawo muku wannan dawuri ba na gaya muku yawan comment yawan typing

Wane mataki mall zai dauka

Da gaske ne Ruwaida tayi abinda mujashid yace

Ya Mall zanyi da halee kyan bariki a gani a gida

*B JATTKO**AMFANIN SOYAYYA*
aure

NA

BATUL ADAM JATTKO
ASHBAT

Kainuwa writers association □□

21

ikon Allah ne yakai Mall w2 yana yin parking ko kofan motan bai tsaya rufewa ba ya shigo afusace cikin reception
din gai dashi ma aikatan suka shiga yi cikin girmawa

yace "manager duba min list wane room Mujashid yakama."

"OK sir na wane rana zan duba."

"na yau Kamar misalin 12pm ."

girgiza kansa yayi yace "Sir ai tun 6 na karbi duty amma oga Mujahid bai shigo ba sai de ko kane meshi awaya k.....

Mall awani irin tsawace ya katse manager
" stupid! kamin aikin da nasaka kawai."

jiki na rawa manager da sauran ma aikatan wajen suka shiga duba list din yau sun duba yafi soba dadi

da kansa ya fuskanci lalle babu fuuu yafita kamar gogowa
Ajiyan zuciya suka sauke daya yace "to yau kuma waya tabo oga Mall ne?
dayan yace "kaide Ciko yi shiru suna lek'en sa har yashike mota sannan su kayi hamdala suka Fara gulmansu

Mall Yana shiga mota yasake kiran Mujashid amma abin mamaki sai yaji wayan yana Ringing a seat din baya
Afusace yajiyo sai kawai yaga Mujashid akance sheme sheme da earpiece akunnen sa yana gyad'a kai idon sa arufe

Hannu Mall yasa zai shako wuyan mujashid mujad da dama yayi ready yayi wuf yaja baya yatura kofa da kafa ya duro waje sai da yagan shi a waje ya fashe da dariya harda rike ciki

Mall kamar zai bude yafito kuma yaga kar yayi abinda zai zubar da kiman sa a inda yake da kima kifa kansa yayi a sitiyari yana wani irin huci idon sa yamasa nauyi

Mujahid lekowa yayi ta Window yace "major mena maka kake son yiwa mommy da my Nafi asara na."?

Mall da yadago kansa sai da mujahid yaja baya dan yanda idon Mall yayi wani irin ja har yabawa mujashid tausayi dan bai taba ganin sa cikin wannan yanayin ba zagawa yayi yashiga motan

Dafa kafadan Mall da yasake zama abin tausayi yayi
"haba my friend yaushe muka fara boyewa juna tsirin mu ne kake shirin boye nin to ni da kake gani dani aka daura auren ka da Aisha Ummi da kanta ta kirani take gayanin nazo a daura amma kai ma baka sani ba kar nagaya maka kaga na rigaka sanin wacece Ruwaida awajen ka dan Sahal ya gayamin komai tsakanin kada Ruwaida ko dama nasanta duk da ban cika zama a

kasan ba ina cikin hotoro na kasa sanin wacece Ruwaida
Ai dazu ganin yanda kabi inda take da kallo kuma yanayin fuskan ya sauya alokaci guda ne yasa na Kalli inda kake kallo ashe itace har kana cewa naje na sameta amma maganan bai kai zuciba dan nasan waye Mall katuna tundaga nursery tare muka fara har kan degree mu na farko kafin kowa yaraba kafa nasan waye kai dama Sahal yace min kanayiwa Ruwaida mugun so kuma gashi nan nima na goda na'

Bari kaji
Yanda mukayi da Ruwaida ina zuwa wajen nace "ah ah amaryar mu lafiya kike tsaye anan duk da munyi lefi mu abokai bamu gabatar da kanmu a wajenki ba saboda yanayi yanda abin yazo mana Amma ama na afuwa ina zuwa da wannan ranan?

Ruwaida kallona tayi rai abace tace "da abin da abokin ka yafada da abin da kai kazo dashi da banbanci. "

Dariya mujahid yayi yace "ashe kinjishi daga nan ya Kwashe yanda sukayi da Mall ya gaya mata

Kuka ta fashe dashi tace "bansan wane irin k'i yamall yake min ba yanzu koni ba matar sa bace a matsayina na yar uwa agareshi Ya kamata yamin haka koda acikin karuwancin nake ballema na shiryu."

"gaskiya bai kamata ba amma ni nasan yana sonki insha Allah wata ran komai zai wuce ai soyayya me tsada kukeyi duk soyayyar da aka masa wannan jayayyar tafi k'argo dan haka ina son duk abin da zai miki ki zuba masa ido wataran kina da riba

Yanzu ina son kibani hadin Kai mushirya masa wani plan din da zamu gane yana sonkin
Kinsan
Hassana kanwar Sahal ko."?

Ruwaida tace Aunty Sana yanzu ma agida na barta ai."

"to matar yayana ce dan Haha zan kirata tazo gidanta
zan kai ki gidan ki zauna sai dare ki koma shima Mall zai dauka muna tare

Yaron da ta aika siyan mai yana kawowa na karbi motan na kaita gidan an mata kunshi da gyaran jiki ka godewa Allah Mall kana da sa a ayaruwa dace da irin su Ruwaida AI.....

"dalla dakata malam kaji a baki na nace maka ina son tane har kaje kake

gaya mata ai ita tasan bana sonta ko zuwan da kaga nayi da gigicewan da nayi dan saboda Kai ne bana son ka hada baki da kazamin bakin ta guntun cancer dako kyan gani babu ba hakori har 2 amma badan nadamu da ita ba."

Mujashid yace "to nagode dan reni hankari."

Hassana ce takira Ummi tace "Ummi kar ki nemi Ruwaida fa wai hayaniyane bata so kanta yana mata ciwo tana gidana ita tasa aka kirani ashe amma nasa an mata komai matar da ta mata aikin har tafi wanda tayi na gida iyawa sai anjima zan kawota."

"to yanzu Hassan tana gidan naki tunda baki kirani ba sai daren nan ga Mijin tama yana tambayanta yanzu yafita a nan."

"afuwa Ummin mu ita tace idan akasan inda taken yanzu su Farida zasu zo su dameta."

"to shikenan sai kunzo."

Borno

Ayya kam sai hamdala dan kowai yayi mata daida a rayuwanta sosai dangin mijinta suke sonta da tattalinta hatta kishiyar ta kwantar da kai tayi suna zaune lafiya dama Maryam kishiyar ta bata da matsala

Balle shi oga da ko ita Ayya bazata ce ga adadin sonda Grema yake mata ba

Kwace take akan cinyar sa rokon sa take akan yabarta ta tafi adamawa saboda shiye shiyen bikin Hamrah

"to wai yanzun me zaki jeyine? bikin da sai on 29
saura fa 2weeks ."

marairaicewa tayi tace "to ai muna wasu shirye shiye ne akwai abin da zan tafi mata dashi da kuma Hajja Batul zata mata gyaran jiki na sati biyu amma ni ko kwana dayane kabari naje nayi ga Barrat ta dameni zan wuce kaduna na kaita wajen Abdallah sai kuma inson samu ne nawuce Kano naga my Ruwa."

"caf kaji duk wannan yawon sai kace shanshani."
Shafo cikinta yayi yace "ban sani ba ko inada ajiya anan a wahalan minda baby kide aika Hajja Batul din namiki alkawarin zakije auren Hamrah sai

kuhadu akanon Barrat kuma zan sa akaita wajen Abdallah dan Abban Ruwaida yakirani jiya ma wai dan Allah akawowa Abdallah Barrat."

Kano

washe gari Ruwaida tasha kuka dan sai asannan akace mata Abban ta har yanzu bai shuce ba akan abinda ta masa ba

cikin kuka tace
"Ummi dan Allah kar ku kai ni dakin aure mahaifina yana fushi dani."

Ummi wayan ta tadauko takira Abban yana dauka ta gaya masa komai tare da bashi hakuri

"shikenan Hjy Ruwaiya amma badan gidan aure zata ba da bazan sauko dawuri ba Amma bata wayan."

Ummi ta meka mata

Kuka Ruwaida ta fashe dashi
"Abba kayafe min Wllh tun alokacin dama bada niyar gaske na.....

"stop AISHA na yafe miki nakuma samiki albarka kuma cikin satinnan za muzo nida Hajja da malama dan malama ta matsa tana son ganin ki."

"Abba malama kuma?

"Eh."
Yace

Haushi ne yasa Ruwaida cewa "to Abba nagode."
takashe wayan ta mekawa Ummi wayanta

Nasiha sosai su Ummi su kayiwa Ruwaida

Abida takama hanuta suka rakata adaidai get Ruwaida ta tsaya t
cek abin ya bawa sau Abida mamaki amma sai suka ji kamar addua take

Ruwaida sai da tayi dogon addua ta amfaci sunan Allah ta daga kafar dama ta shiga bakin ta dauke da addua har zuwa bedroom dinsu kokarin zaunar da ita Abida tayi amma taki zama

"Aunty abeed zan dan shiga bathroom."

Dariya su Kharajina suka ai dole cikin ki ya kad'a wannan k'iran na yamall

Aunty Hassan tace "bama son rashin kunya fa Nafi ku fice mana."

Farida tace caf "ai muna nan sai munga kokof."

Abida tace "a kofe kude inde yamall ne

Ruwaida alwala tayi tafito tace "aunty abeed ina sallahn da daddy yabani dama yana hannu Ashur kanin Farida har Qur ani da shijab ta karba ta tada ikkama tayi rakk'a 2 tare dogon addua har su abida suka gaji sukace mude zamu tafi kar wannan mugun ya taddamu dan dare yayi

Nafi tace "wai ita y'ar iska dan mubar mata gidan tane tawani share mutane ta dauki karatun munafurci to Wllh gobe da safe anan zanyi break."

Haka suka karaci mata tsiya su

Suna fita Ruwaida ta fara jin wani mugun ciwon mara wanda na period ne dan tana shan wahala gashi dama doctor ya hanata shan kowane magani acewar sa zai iya mata wani illan tunda shekarun ta yakai na aure tayi shine samun saukin ta saide tayi ta han ruwa mezafi dan samun sauki da wuri

fitowa tayi general Parlour na kasa dan ko zata samu ruwa dan kitchen din saman taga fanfon yaki kuma bawani alaman ruwa aduk fridge din

Tana fitowa ta zube a kan kujera tana dafe da maranta

Mall badan yanda Ummi tasa ido akan saba ba abin da zaisa yatare part din nan batare da Haliman saba

tana kwacen yazo ya wuce ta yashiga

Bayan yafito a toilet ne yagama shirin komai nasa yaja wayan sa zai tura wani sako ta email duk akan ashirin auren sane

Message yake ta shiko masa ta whatsapp sai da yagama abinda yakeyi

yashiga WhatsApp din bakon number yagani
Shiga yayi yaci garo da abinda ya firgitashi

Kamar haka harda video

Mall me Sa a ko nace me sakaci ka ari mace me kyu bayan hausawa sunce mace me fasale ko tai aure bata dan gana ba kai ko ita ta dangana mu Mosoyan ta basu dangana

Sai ya danna video din
Kansa ne yafara zuyawa amma yana cigaba da kallon yanda Ruwaida da Affan suke romance na mugun watsewa kuma a zir din su suke adaidai sanda Ruwaida ta kamo gaban Affan zata sa abaki

wani irin k'ara Mall yasa tare da mekewa kawai tsintan kansa yayi a parlour inda Ruwaidan take kwance bai karasa ba ya jefa mata wayan sai da yadaki goshinta ita ma k'aran tasa dan ko bata duba ba tasan ya fasa mata goshi

"kidauki wayan kigayawa kwarton ki ni Ismail Wllh na wuce kuntun su dan haka yadena bawa kansa wahala wajen turomin k'azanta cikin waya idan ganinki yake so yayi yane ma muku inda zaku na haduwa bani da damuwa."

yana gama fadan haka ya haye sama

zubewa yayi a gado yana wani irin numfashi abin tausayi

Ahankali cikin ma wuyacin hali ya furta
```Ummi idan kin rasani dalilin Ruwaida ne ai kinga irinta ga abinda yasa na hakura da ita ya Allah ka d'auke rayuwan baiwar ka AISHA dan zuciyar bawanka Ismail ta samu sauki ko kadauke nawa na huta```

Ruwaida saida taji rad'adin goshin yadan lafa ta dauki wayan da har lokacin videon ne yakeyi

"walahaula walakuwata illahbillah!."

Affan dama duk zamanda muke da kai daukana kake kana adanawa nashiga ukku ni AISHA zinah nadena ka baka dena bina ba duk da haka ba zinah nayi gaba daya ba
Asttafullah kuka take sosai tunanin bari takira mommy sa ta gaya mata abinda Affan yayi baikyu ta ba tayi dan tana da number ta Akanta

Sallama mommy tayi tace
"dawa nake tare."

cikin rawan murya Ruwaida tace "mommy nice."
```

"Ruwaida yawwa ai dama nemanki muke ido rufe saboda munfara aikin mu amma sai da hadin kanki zamu samu nasara da gaggawa yanzu haka ga son nan munturawa Ismail sak'o muna jiran Ripley ne ke kuma akin da zan baki sai mun hadu gaba da gaba dan haka ki san yanda zakiyi ki samu ki fito cikin kwanakin nan biyu
kuma dan Allah kar ki yarda ko hannunki Ismail ya taba dan ga son nan tunda yamma yakasa cin komai wai idan Ismail ya kusanceki bazai iya rabuwa dake ba
gashi ma Affan dinki dan lallasheshi.....

"Hello my love. "

"Affan kana tunani abinda kamin shine soyayya yanzu kam banyi nadaman rasa kaba sai ma godewa Allah dan ku ba alkairi bane agareni."

"what Affan ne fa my love menayi miki."

"ashe Affan duk zaman mu dakai muna furtata kake kana daukana a video dan wata ran katuzarta rayuwa ta ko kamar yanda kayi yau."

Affan yace
"ada banyi da niyan wani abu ba kawai idan ina wajen aiki nayi missing naki idan na kunna nagani sai nasamu nusuwa yanzu haka na kunna ina kallo ina kuka mommy da tagani tace ai wannan ma makamine na turawa Mall kinji yanda akayi."

"Affan Wllh sonda mommy take maka zai kaiku ga halaka kuna rayuwa sai kace na ya hudawa nik...

Kar ban wayan mommy tayi tace "Ruwaida idan na fashimce ki kamar bazaki bamu hadin kaiba ko to Wllh idan kina shirin haka ma kiyi.....

"dakata mommy dama da hadin bakin ki Affan yamin haka na cire Affan a sawun masoyana masoyi bazai min abin da yamin ba dake da danki kufita min cikin rayuwa."

Tana gama fadan haka ta kashe wayan

Tashiga video din tayi detele din komai

Tsaban bacin rai ciwon ma rasashi tayi ajiye masa wayan tayi ta haye sama dan yanzu ita ma kunyan Mall takeji zata guji duk hanyan da zai hadasu

Bayan sati 2

Ruwaida da Mall tunda abin yafaru ba suga juna ba gashi har gobe dauren auren sa da Halima Sahal da Hamrah

abangaren Affan shida mommyn sa sai abinda yakaru suna shiri sosai dan ma sun rasa number Mall dan wanda suka turo na farko bai sake kallon inda wayan yake ba

Ruwaida tana babban gidan ana ta harka kannen ta sunzo ga Barrat har da Hajja

Khalifa ne yashigo
Ruwaida tace "ya khall yaushe kazo."?

"Lill momy ai tunsan da kika k'ule a gidan ki kika manta mu."

Dariya Ruwaida tayi tace "sorry yakhall Wllh ba waya a hannuna kuma lefin su Nafi ne ai kullum muna tare."

ganin wawulon Ruwaida yasa Khalifa ya dafa kansa alamun yayi mantuwa
yace "kahs kinga ko nakusa na manta doctor kin fa yamin waya yace zuwa yanzu za a iya miki aikin hakorin dan haka asa ranan komawa asa miki."

"yawwa yakall kamar kasan Wllh amatse nake ko bakina bana son budewa gaba daya."

Dariya Abubakar k'anin Sahal yayi
yace "kaci uwar gida wato kina tsoron amaryar mu tazo tana renaki da wawulon baki ko."

hararan sa Farida tayi tace "ai Wllh yabull ko duk hakorin ta rasa Wllh wuce nan wannan me bakin fuskan tarena ta."

Abubakar yace "ban da ky'ashi ai naganta a colander tas take."

Kharajina tace "caf ai Wllh kos korimace Wllh Laraba me aikin Mama tafita kilin gata daf da kas'a kamar tukuban tsire."

dariya akayi taci dan walwala family akwai fashimtan juna

Washe gari da misalin 9 na safe aka
daura auren

Ismail Muhammad Muhammad

Da HALIMA

Saboda za aje Adanawa adauro da Hamrah da Sahal

Ruwaida tace Ummi dan Allah nima naje Adamwan idan andaure sai muzo tare."

Ummi tace "wannan mijin ki zaki tambaya shiyake da iko."

Shiru Ruwaidan tayi ita ko ina zatabi hanyan da zai hada ta da Mall ma

Umman Ruwaida tace "to yaya abinda ita ma Hamrah nan zata zo me nata na zuwa muma manya ai godiya da karban amarya ne zai kai mu."

Kowa baki ya fude yake kallon yanda Ayya Hamrah Ruwaida suka dau makeup
dan wanda yamusu mekeup din ya kware sosai dan hatta kaman su iri daya ya maida kodan komai nasu iri daya ba ban bancin takanas a *India* Abida tayi hayan sa dan yayi musu mekeup din

Haka suma Nafisa Kharajina Farida shigan su iri daya gasu dama duk farare kyawawa suma

Sai aunty hassana da anty Fati da Aunty Abida suma shigan irin daya
Duk material ne

Sai yaran gidan dana dangin suma kowa duk anko iri daya maza da matan su

Ihu su Kharajina suka sa asanda suka ga su Ruwaida Wow sis
KALA KALA KALA ABASU KALA

Abida tace "gaskiya kam yau suka amsa sunan su Aisha ukku masu baiwan kyu Na BALAI
EN UKKU
yawar daya yar uwa hakori."

Fati tace " kar ki bude baki dan ma nasan ki da kamewa."

Hall din ba lefi yahadu Halima ana zare ido dan anzo wajen dako amafarki ba asan za azo ba ita ma balefi tayi kyu dan Mall ya kashe kudi sosai wajen daukan masu yimata makeup

Mall zaune da amarya sa
Sahal ko har yanzu zaman jiran isowan su yake

Wayan sa yazare yakira Abida yace "ke Abeed bana son wasting time ."

Hamrah da Ruwaida
Awaje suka barsu

suka fara shiga DJ din Abida tayiwa magana akunne aiko ya sako wani lafiyeyen kida wanda baitin wak'an Rara ne yake rerawa adaidai sanda Ruwaida ta shigo Hall din tare da wasu indiyawan yan mata daga bayan ta suna zuba mata wasu yan kakkun flavour masu kamshi

Asannan sautin wakan yayi k'arfi kunsan de rara ga kadan daga cikin wak'an

kuzo mu wak-e amarya ango yaji dadi kauna idan tayi nisa riba aure

wak'an ya bak'an tawa Mall rai dan sunan sa dana Ruwaida kawai aka sako ba asa na Halima ba amma yasan abida ce

Daga nan Ruwaida takoma tazauna acikin yan uwan ta dan bayan da satayi ta hau inda ango da amarya suke dan ba a tsara zaman da ita ba

Kamar yanda Ruwaida ta shigo haka Hamrah ma ita ma nata wak'an yayi amma Ali jita ne yabudo

Duk marokan da sukayiwa Hamrah da Ruwaida kirari Ayya kyutan kujeran makka ko key din mota take badawa ai take waje Ya kacame da aka san cewa Ayya ce
A K D
kuma Ruwaida yar gidan me kwano ce

Halima da yan k'awayen ta yan kallo suka zama Mall da yaga duk shirin na kankan tar masa sahibar sane hannun ta yakama suka fita

"Ismail da ma Ruwaida ce matar ka yan ukku balai da baba yake aiki agid.....

dasauri ta rike bakinta dan takusa kwafsawa

Mall yace "ki karasa mana baban ki yake aikin zagin su agida kullum ko ai inaga bawani malami da bai zagesu ba."

Sai asannan ta samu bakin magana tace "Eh Wllh amma mamaki na ya akayi tazama yar gidan me kwano kuma meyasa kuke kama da ita?

"zan gaya miki kinga yanzu abokina yana kirana bari na gansa shiga mota yabude mata

yana barin wajen k'awarta Baraka da take boye tafito tace "ke Haly anya baki cusu kan ki inda yafi kar finki ba ki duba wadan nan larabawan ki shigo cikin su Wllh in badan abin namiji ba ko a yar aikin bazai kai ki gidan sa ma me kamar wannan matar de kaga yar me kwano da yafi shugaban k'asa kudi."

"Baraka kede bari wllh babban Matsalan ma kin san baban mu agidan su yake aiki drive din sune dan ma bawanda yasan ni y'arsa ce ni wani kyansu bai dameni ba tunda shi yagani yace yana sona ai yasan da ita ni ya
ce yana sona."

"ummmm nede ina jiye miki kishi da abasu kala

Adaren aka kawo Amarya Halima

Mall sai rawan jiki yake dak'yar yabari sukayi sallahn godiya

Amma me yana cikin shafata hannun sa yakarasa cikin bra din ta memakon yaji dum kamar yanda yake sammani sai yaji Abu luguf a kance gashi bawani tudu duk da shidin bak'on abin ne yayi mamaki dan ayanda yake kallon Boob's na Mace yana ji ajikin sa idan an taba za aji wani yanayi dan kallo da ido ma yana jefashi cikin wani hali idan yagan su kyam a tsayen tunba na Ruwaida

Amma ya share yaci gaba yaje kan me gaba daya wani ihu Halima tasa tana yarfa hannu sai gumi tage tana ihu ganin haka yasauka amma sai me jinin da yagani har yayi yawa har tsoro yabashi amma yayi murna tunda ance duk wacce ta fitar da jini a first night to takawo budurcinta
Tasha tarairaya awajen Mall amma ita ta kanta take dan zafi takeji sosai
Adare suka tafi asbiti

" doctor ban gane dinkin da aka Matane yafarke ba wane dinki kuma za ayiwa gaban macce kuma budurwa."

"Mall dinki aka mata bai kara sa warkewa ba wajen ya farke a haifuwa ne aka mata dinkin kome."

" wane irin magana ne Doctor jiya muka tare da ita dan naga baka gane ba."

What? Sir kana nufin wannan raunin a first night tasamu to ba haka bane asalima dinki aka mata bai karasa warkewa ba har wajen yafara b'aci kuma

wannan ba budurwa bace dan naga wani tsohon operation na haifuwa a k'asan maranta in ma da sunan buduwar ka aureta...

Bai karasa ba mall yazuba masa wani wawan mari tare da sake shak'o wuyansa

"matar da na sameta mudurwa zaka ce har ta haifu kasan yanda nake da kishi kuwa."

"sorry sir muje na nuna maka kagani da idon ka."

Tunkuda doctor mall yayi sukaje har dakin da Halima take akwace

Doctor safan hannu yasa tukun ya budewa Mall zanin da Halima ta rufu yace kaga ga kan dinkin nan wanda ko warkewa baiyi ba

To kaga operation din nata kuma tabbas na haifuwa ne yakamata ka bincike ta dan da yawa mata idan zasuyi aure suna zuwa mu musu Dinkin ni da kai na nasha yiwa mata."

Cikin wani irin tsawa Mall yacewa Halima "ki gayamin gaskiya ya akayi aka miki dinki dakuma operation na haifuwa?

Kuka Halima tasa tace "Wllh tsautsayi ne Ya fadamin wata rana naje Iban....

Tofa

*B Jattko**AMFANIN SOYYAYA*
aure

NA

BATUL ADAM JATTKO

NA HANA AMIN DOCUMENT AMMA YANA CIGABA DA YAWO

Kainuwa writtes associate□□

DOMIN KU NAKE MASOYAN ASALI

AYSHA GARKUWA GROUP NVL

JATTKO GRP NVL

KAINUWA FANS

ASHBAT JOOTGAR FANS

HUGUMA CONVERSATINS

SAWWWAMA GRP NVL

SUBAYA GRP NVL

AZRAA FANS

MEIMEI BEE FANS

MRS OMAR NVL

AISHA MACHIKA FANS

AISHA SADA GRP NVL

SADNAF GRP
SAJIDA MALL YAJI SAKON KI

RALLY GARBA K"AWAR HALLYMALL □

DA DUK WANDA SUKA BADA SAK'O NA ISAR

DAN KUNA BANI KALA A COMMENT DIN KU□□

22

naje gidan kakata a *K'ofan na isa* ta aikeni na ebo mata ruwa a makota zata tafasa tea dan rijiyar su ba dadi nasamu wani Yana jan ruwa kawai sai nace bari na zauna akan boket din kafin yagama zaman da zanyi ashe a tsinin bakin marik'in bucket din na zauna ya shigeni sosai dan kasa cire min ma akayi sai a asbiti aka cire aka min dinki shine lokacin da nace maka nayi tafiya Tarawa kaiwa alewan bikin dan ina jin kunya gaya maka ina asbiti ne."

Operation fa inji Mall cikin tausayawa dan ya gamsu

"tun ina yarinya nake da matsalan fisari a marata amma ina kara girma abin yana karuwa har sai da aka min aiki na samu lafiya".

Doctor Khalid shiru yayi yana jin renin hankalin Halima amma da yayi tunanin idan ya tona asiri zai iya b'ata sunnah shine yayi shiru

Mall yakali doctor yace" kaji ai ko."

"Yes hakan ne Sir".

matsawa Mall yayi kusa da Halima Ya gyara mata
zanin ya zauna a bakin godon cikin tausayawa yace " sweet meyasa baki gayamin ba nasake jimiki ciwo."

Halima Jan mayafin ta tayi tarufe fuskan ta alaman kunya."

Mall ya kalli "doctor yace" yanzu doc yaza ayi."

"Eh zamu mata aiki a wajen dan haka zamu dan riketa kwana 2 saboda sai muna dressing din wajen. "

"OK. "

Part din Su Sahal

sosai yanuna kulawan sa akan ta yana wani rawan jiki kamar buduwar zai bude dan yasan Hamrah san me zafi ce ko acikin mata daban take watan nin nan bashida wani nusuwa dauriya kawai yake

"Allah yasall nafa koshi."

"Hah daga kincin ye wannan zan kyaleki. "

bude bakin tayi yasa mata

mek'ar da ita yayi tsaye yana warware mata leffayan da Ayya ta nade ta dashi yana lumshe ido dan yanda wani lafiyeyen kamshi yake tashi ajikin ta jefar da liffayan yayi doguwar rigane ajikin ta hannu yasa ya zuge Zip din rigan yayi k'asa sai bra do sket ya dora hannun sa akafadan ta yana shafawa ahankali har zuwa inda k'arfen bra din yake balle shi yayi shima yayi k'asa a hankali ya aika hannun sa kan boobs din idon sa alumshe yace "Wow sugar yan watan ninan da bamu gaisa da mutane naba suka girma haka suka kara laushi sugar a duniya Allah ya zabeni yacika min burina Allah yasa a lashira ma nasamu irin wannan rayuwan."

Ita de kuka takeyi

Yace "yi kukan ki sugar Yau ranan murna ne."

kwace jikin ta tayi tazube a kasa tana kukan sosai

cikin kuka tace "ba kukan farin ciki nake ba Sa I'd kukan bakin cikin ne bani da abinda zan baka na murnan wannan ranan dan nasan Yana cikin ranakun da baza ka mantasu ba naso ace ina da abin baka amma Nura yacutar da rayuwa ta."

tsugun nawa yayi ya shafo hawayen ta
"idan dan wannan kike kuka AISHA kibar kuka kina tare da Sa adun ki nefa wanda yafi kowa sanin ciwon ki
wanda AISHA kawai yake so bawani abu naki ba dan Allah idan ba kukan dadi ba kar ki b'ata mana daren nan dan ni sonake mu manta da komai sabon rayuwa zamuyi bana son ki kara kawo min baya Hamrah ina kishin ki dauki kanki bawanda kika sani sai ni nidin ma Kai na kishin kaina abaya da bamukai matsayin aure ba nake dan haka ki dauka yanzu zaki fara sanin Sall din ki."

da ganan ya hade bakin su suka zube anan cikin nuna kewar juna

Allah yakawo zaman lafiya ina yiwa duk wanda suka tsinci kansu cikin rayuwa irin na Hamrah aduar shiryuwa da samun ingan taccen rayuwa yaku ma kare wasu da shiga irin said Ameen

Umman Ruwaida ce takira Mall

Yana dauka yace "Ummati an tashi lafiya."?

"lafiya lau d"ana yara sun kai muku Breakfast sunce baku sauko ba shine nace ko su haura saman kar abar yar mutane da yunwa."

"Umma ai bamu kwana agidan ba muna asbiti da Halima."

"subbahanallahi!!! meyasame ta?

"Umma sai de kunzo din kawai ."

abin yabawa Ruwaida mamaki wai Halima a first night taji ciwo har asbiti amma data tuno maganan caballiya na zuwa wajen di'nki tayi murmurshi tace za arina

Umman Ruwaida ce kawai taje ta duba Halima a gurguje dan jiirin safe zasu hau zuwa kaduna daga nan ma airport ta wuce dansu Kharajina da Farida suna jiranta

sai yar aikin Ummi Saratu aka barwa Halima

Mall yakira Ummi rai ab'ace

"haba Ummi yanzu kamar matata ba lafiya duk gidan arasa wanda zai zauna mata sai yar aiki."

"yar aikin ba mutum bace
To ma wakake son natura Abida Hasana Fati de kasan matan aure ne tun ajiyan Hasana da Fati suka tafi yanzu Abida ma shirin tafiya take Abuja

Kharajina da Farida sunbi Umman ku kaduna
Nafisa kuma shirin tafiya suke india gobe zata raka Ruwaida za asamata hakori ko dan ita Ruwaida baka damu da halin da take ciki ba

Ita matar taka ba yar gari bace bata da dangine za kamin iyayin naka da kake ganin kafi kowa iko ko."

"Ummi amma.....

Ummi kashe wayan tayi

Har aka sallami HALIMA Ummi bata jeba Umman Sahal da Mama Farida ne ma sukaje so daya

Su Ruwaida anje andawo hakori ansa kamar dama natane kuma ba me cirewa irin namu nanan aka sa mata ba shi yashiga kenan har mutuwa

kwanan ta Ukku a part din Ummi Ummi tace ta tattara ta koma nata

Langwabe kai tayi
Tace "Ummi wai da Sai naje kaduna na dawo tukun."

murmurshi Ummi tayi tace "kide koma dak'in ki tukun zakije kaduna kwanan nan."

Nafi ce kadai taraka ta dan su Kharajina sai gobe zasu zo a kadunan

Halima da kawayen acike a parlour tana ganin su Halima da gudu tayi kan Ruwaida ta Rungume " oyoyo Aunty ai ina tambayar ki awajen Ummi take cemin kinyi tafiya dan sweet haka yace min bai sani ba da na matsa masa ma yace idan ina son zaman lafiya dashi karna k'ara kawo masa zancenki ni kuma duk banji dadi ba kar ace ko adalilina ne yasa zaki bar gidan dan bansan ma Mall yana da mata ba sai ranan bikin."

Ruwaida kokarin raba jikinta tayi da Halima dan duk maganan nan tana rungume da Ruwaidan take yinsa gashi kuma taji ance y'ar lesbian ce dan sai faman gogata take da jikin ta
Ruwaida raba jikin tayi ta b'ata fuska tace "nagode.

Suka haye sama Nafi tace "nifa matar yamall din nan bata min ba."

Ruwaida tace "shi ai tamasa."

HALIMA tana komawa kawar Baraka tace "amma kin more ina ma nice na rungume lafiyayyeyan jikin nan."

Hafsy tace "dan Allah Halee kisan yanda zakiyi kisata a kungiyar duk mu d'ana."

Halima tace kun isa ma banzaye ai tafi karfin ku har kunsa nafara kishin ku

da safe Ruwaida parlour kasa ta sauko cikin shiganta mekyu da aji duk da bawani mekeup tayi ba wandon jens ne sai wani roba roban riga kuma Shara Shara ce rigan ana kallon boob's dinta gashina afili suna wani irin zillo ga

heeps na daukan hankali tana kad'asu kanta ba dankwali sai zubo gashin ta da dama ba kitsuwa yake ba da tayi abayan ta gashi yasha gyara a India

samun su tayi a zube manne da juna amma da gani Halima ceta manne masa danshi aikin sama yake a laptop dinshi

"Assalamu alaikum
Yamall barka da war haka. "

tace tare da zama akan kujera ta dauki kafa daya ta daura akan daya

Mall da yake son yayi control din idon sa kasawa yayi kasa dauke idon sa yayi akanta amma duk da haka Halima har tafishi shiga wani hali wuf ta tashi tana fara a
"Aunty wllh har na manta da kina gidan ai da nakiraki munyi breakfast amma tashi muje kidan ci wani abu tayi maganan tana hada hanunta dana Ruwaidan."

Ruwaida tana da k'ank'ami dan ba abincin kowa take ciba tafi ma ga newa tayi da kanta dan ita abinci me nauyi bai dame ta ba babban abincin ta me nauyi bai wuce dambun kuskus ba sai kunun k'yada ko nono kuna kafin ta tsako tayi shayin buri da na'na' da cukui tasha bata da wani abincin da yawuce wannan."

Ta janye hannunta tana cewa
"bana tare da yunwa."

Ta Kalli Mall da sai lokacin yake kokarin janye idon sa akanta amma yamakara dan sai da suka hada ido

Tace "yamall ance Hamrah bata jin dadi zan dan shiga."

idon sa akan laptop din sa Kamar bazai bata amsa ba de yace "da da zakiyi tafiya har na barin kasan da izinin wa ki kaje ."?

"ai nazaci su Ummi Sun gaya maga."

bai kalleta ba yace "ok yanzu ma sai kije ki aiko Ummi ta gaya min."

Ita de Ruwaida jan bakin tayi tayi shiru

Halima tace "haba sweet ka barta mana."

Hannu ya daga mata alaman baya son maganan

Adai dai lokacin Kharajina da Farida iyayen hauka suka shigo da gudu Ruwaida ce a facing din kofan dan ita suka gani

"Wow sis haka kike bada kala abasu kala abasu kala."

Suka fada jikin Ruwaida suna cigaba da ihun su

Wani irin tsawa sukaji
"Kai waya gayamuku nan dandalin karuwai ne zaku kawo mana iskanci
Get out ."

da gudu suka fita jiki yana rawa dan su basu kula yana gida ba

Bayan wata 2

Mall da Halima iskan kala kala suke yi agaban Ruwaida bawani kalan romance da basayi
Agaban ta

a ban garen Halima tana yine dan Ruwaidan taji haushi tunda Allah yagani mugun sha awan ta take amma Ruwaida tak'i yarda koda hannunta ta taba

Shima Mall hakan ne mugun sha awan Ruwaidan yake Dan ko bai taba ba yasan Ruwaida da Halima da bambanci dan Ruwaida tanayin shigan da yake bai yana tsirinta sosai

yanayi ne wai dan yajefa Ruwaidan cikin wani hali idan ta matsu zata kawo kanta gareshi Dan yanzu ya gama tabbatarwa lalle sha awanta yakeji so dayawa ko aiki baya zuwa saboda kawai yaga tafito ya ganta

Hamrah ce tazo dan kullum idan sahal ya fita office ita ma nan take zuwa
dan Mall baya barin Ruwaida tafita

Hamrah tace "anya Ruwaida kece kuwa anya ba acan zamin ke ba wllh nagaji da jiran yaushe zanga farin cikin ki alokacin da Sahal yagaya min an daura auren ku da Mall kuma baya son ki wllh cemasa nayi yazuba ido yabamu wata 2 kacal zaki juya Mall yanda kike so amma ina sai naga kamar yanzu basiran ki ya toshe gaba daya sai kace ba Ruwaidan mu ba."

"Ya zanyi ne Hamrah nifa bama wannan ba yanda yake nunawa matar sa wani kulawa da soyayya agaba na wllh yanzu har tsoron fitowa general parlour nake saboda sex ne fa kawai basayi agabana duk wani kala romance

wllh bawanda basayi."

Hamrah tace "banza to ai dan ke sukeyi dan kiji haushi yanzu da kika dena fita general parlour ai dadi zasuji Suji sun san cewa kin damu ki fita kinuna baki damu ba ki din ga yin shigan da zaki na daukan hankalin sa shifa namiji ne wane lafiyeyen namijin ne zaigan ki baiyi sha awanki ba haba sai kace bake ba kikayiwa bariki ma kwalliya balle aljanan ki
keda hatta cibiya baki bari ba kina masa kwalliya

kiduba wannan matar me dunkulelen wuya Wllh ko a ayar akin gidan nan bai kamata ta zauna ba."

Haka Hamrah tayi ta bata shawara tako gamsu

Gidan su Affan

"haba son kaga yanda kake son hallaka kanka wai idan kyan Ruwaida ke fusganka angaya maka mekyau suna karewa ne najima inason baka shawara akan abinda sai yafi maka Ruwaidan alkairi kaki."

"Mommy menene zaifi abinda raina yake so alkairi. "

"yawwa son ina son na maka tayin Kharajina kaga yarinyar tana da hankali da nusuwa gata budurwa gashi bawani abinda Ruwaida zata nuna mata yarinyar tamin tun sanda mukayi zaman jiyar Ruwaidan kuma naga kaima ai da shakuwa sosai a tsakanin ku duk ko inda shakuwa yake to idan am matsa so zai shigo son ka daure a kullun sai nayi istihara a kan ta akullun sai naji son ta yashigeni ina ga akwai alkairi."

Shiru Affan yayi
Ganin bai musa ba yasa HAJIYA HADIZA tayi ta cusa masa ra ayinta

Numfasawa yayi yace "mommy bawai bazan iya sonta bane bana son nasake yiwa zuciyata tabo saboda Kharajina tanada saurayi matawalle dan gidan tsohon Kaduna state governor. "

"bar wannan Affan kaide kaje ka kwada ina ji ajikina za asamu sa a."

wayan Kharajina jina yayi ringing a karo na 3
tana duba me kiran ta dado kai ta Kalli Ruwaida

murmurshi Ruwaida tayi tace "sarkin munafurci ki picking mana Kharajina kina son boye min kuna soyayya da Affan duk da bansan dalilin kina boye min

ba."

sunkuyar da kanta Kharajina tayi tace "wllh kunya nakeji ace saurayin yar uwata....

"dakata my kharaji nida Affan de kinyasan munrabu Kennan wllh bana fatan rabuwa da yamall dan shine zabina da sonsa na ginu

Affan yayi arayuwa Ya iya soyayya sai dena miki murnan samunsa Allah yasa shine mijinki."

"Ameen. Inji Kharajina

Ruwaida tace "sai de matawalle fa ya zakiyi da soyayyar sana shekara 7.?

"Gaskiya sis matawalle fa mommy sa tana da matsala ba muna cikin soyayyar ba tace ita d'anta ba zai aureni ba saboda ai ba asan asalin Ummi ba
Dama yamall ma yace idan nasamu wani nayi aurena kuma Allah yamin zabi da mafi alkari yabani suruka mesona dan mommyn Affan fa kullm ita take tashina sallahn asuba dan ma basai nagaya miki wacece itaba."

Mall da Halima suna fitowa acikin super market bai fita da escort dinsa ba daga shisai Halima
Suna tafiya sai wasu samari da suka sauka akan babur da alama ciki zasu shiga

"Kai Kai wanake kamar *kyan bariki*?
dayan yace "itace mana halee kyan bariki haka abu yaci gaba yanzu andena bin Kallamu dan garuwa kenan."

Halima yitayi kamar bada ita suke ba

"haba halee kin bata bat uwar daba kashe arna wllh goron dutse sai uwar daba me arna."

da sauri ta taka tashiga cikin motan

Mall yana juyowa samari a tare sukace "M W W!!!!
ai ajuje suka arce dan ganin yanda fuskan sa yakoma

bayan yashiga motan zuciryar sa tana masa tsake tsake dan ba wannan ne karo na farko da hakan ta faru ba duk sanda yafita da ita sai hakan yafaru why?
Amma baya son zargin kowani abun yayi tasiri a ransa

cikin dakiya yace "Sadiya. "

cikin rashin gaskiya tace "naam.

"meyake faruwa ne aduk sanda muka fita sai hakan taso kasan cewa dake awancen karan na miki tambaya kince baki sani ba ko
bawai dan nayar da ba na Kyale awancen Karon ma dan ance ruwa baya tsami banza
ki gayamin meyasa samari da matasa suke miki kirari da halee *kyan bariki* da kuma *uwar daba me arna*?

Kuka na muna munafurci tasa
tace "kasan ni naci sunan kakata
ta bangaren uwa akwai yayan Mamata a goron dutse kamansu daya da mamata haka yasa mu yaran suma muke kama sosai kamar de yanda kuke da Ruwaida to akwai wata yarinyar ta Halima wanda sunan mu daya ita ma sunan kakar mu ne da ita yariyar ta mana zakka a family.

Daka nan ta kwashe duk yaruwanta ta gayawa Mall da suna yar uwar tace

Takara da cewa shigasa ina budurwa nafi sa nikaf idan zan fita musamman idan zanje goron dutse gidan yayar mamata."

Mall ya gansu da mayanin ta

Yace "ashe kuma kuna da zakka to Wllh kar ki bari tasan hanyan gidan ki
dan wanda na ajiye a gida mata ta isheni."

Tace" insha Allah."

